Darajar Yayana2-01
Posted by ANaM Dorayi on 09:52 AM, 20-Mar-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
___________________NA
___________HALIMA K/MASHI
Assalamu'alaikum, barkanmu da warhaka fatan kuna lafiya,nasan kunjini shiru a cikin wannan littafin,lallai kam kusan incemuku babu wani kwakwkwaran dalili face rashin kulawa daga gareku,saidai dayake ni nayi niyya dole incigaba,da wannan nake bawa masu yawan bibiyata hakuri,In Allah ya yarda da sannu zamu kai har karshen littafin,
Na tashi na shiga wanka ina yan kun kunai,ko kallona Iya bata yi ba, sosai nayi gayu atanfa fara da sirkin purple ne. Haka takalmana da mayafina duk purple ne, na fesa turaruka sosai.Iya ta kalleni ta ce, da ma na san kun hada bakine shi ne za a gwada min bariki, in dai namijine kuje Allah ya taimaka. Ni dai nayi sororo raina babu dadi, sannan bani da mifita.Har cikin gida Usman ya shigo suka gaisa da Iya, sanan yace zamuje ne ta gaida Ogansu Aliyu.Iya ta ce, menene na shirya karya Usman ku da matarku.Nina haifeku fa har da kukega zaku yi mun wayo, a gaida Gyambo karshen girma kenanko? Usman ya sunkuyar da kai yana dan murmushi cikin jin kunya, ni dai na ce sai na dawo.Da mota yazo na shiga, gidansa muka fara zuwa ya ce inga Abida matarsa minti biyu. Ina yin sallama ta amsa, sanan ta ce kai Amarya kin tsula kyau sosai, taja hannuna zuwa bedroom din ta. Zo muyi yar shawara,Bakin gado muka zauna.Ta kalleni a da banyi zaton zaki zama mai taurin kai ba.Na zaro ido ina kallonta, ta ce, ranar juma'a da daddare mijiki nan ya ci abinci tare da mijina, ina daga ciki ina juyo su mijinki yana fadawa mijina halin da yake ciki na takura.Gashi kinki ki bashi hadinkai, har yana cewa wani dare da kika ki sauraranshi har ya dagawaya ya kira wata yar sanda dake nacin sonshi ta kuma sadaukar da kanta gareshi.Har ta daga sai kuma tsoron Allah ya shige shi, Allah ya taimaka ya tashi ya shiga yin

nafila, daba dan haka ta faru ba, me kike tsammani?Na ce, wai Allah, daga nan sai zina.Tace kina da kwamasho ko baki da shi?Na ce, ina dashi.Madallah.Ta dafani yanxu abinda nakeso dake, kinga ke yar zamani ce, ki rike mijinki, in ba haka ba sai wasu su rike maki shi.Na ce, anty iya ce, Allah ba dan Iya ba zanyi duk abin da yake so.Ta ce, to baga shi yau zaku fita ba, in kin dawo Iya ganewa zatayi?In ba ke kika fada mata ba.Nayi shiru ta ce, to kisani kina cikin tsinuwar ubangiji, in yanxu kika mutu mijinki yana cikin wanan halin sai kin hadu da fushin Allah, ma tsawar ba shi ya yafe maki ba.Gabana ya shiga faduwa, na ce, Allah anty nitsoro nake ji ban san yaya abubuwan suke ba, nima bansan yana fushi dani.Tayi murmushi ba wani wahala.Ta girgiza kafadarta, ki amince da mijinki a duk lokacin da ya bukaci haka na rokeki.Na raunana muryata, in na sa muku aure ba?Na ce eh.Ta ce ki ceci kanki daga halaka fa, kin san komai ke ba jahila bace....Muryar Usman ta katsemu da cewa wai me kike kitsa mata ne?Zo mutafi kinji.Ta ce, jeki kada yajimu basusan naji firarsu ba, dan Allah ki kama mijinki hannu bibbiyu ko bakya son shi?Na sunkuyar da kai ina sonshi mana, bari dai in gani ko zan iya ina tsoro.Na fita muka tafi.,ban san ina muke tafiya ba, don kaina yana sunkuye ne ina wasa da yatsuna.Har zuwa lokacin da motar ta tsaya.Ina daga kaina COMMAND GUEST na gani.Ya ce jirani kadan ina zuwa.Gaba na ya shiga faduwa, koda ban san ko inane nan ba na tabbata Hotel ne tunda naga an rubuta guest.Bayan wasu lokuta ya dawo yana waya, danhaka da hannu ya yafito ni, na fito a baya nabishi yana ci gaba da tafiya tare da tin waya.Kuma na fahimci kamar da ya Aliyu suke magana, dan naji yana fada mai ga mu nan yanxu zamu shiga cikin hotel din.Kuma ni zan wuce ne dan Allah kayi hanzari muka ratsa falon muka nufi jerin dakuna yasa makulli yana bude wani daki.Dai dai lokacin sako ya shigo cikin daki wayata, na ciro na duba.Cewa yayi kishiga kijirani kadan my choice.Na kalli Usman yayi

murmushi ba da jimawaba zai zo, yanzu zaki
ganshi.Na shiga cikin dakin ina dari dari, tare da
yankalle kale, ya tako ya shigo dakin.Kada ki
damu ya dauki remote ya kunna TV, kiyi kallo ga
tashar India nan abin sonku mata.Ya nuna mata
wata takarda.In kina da muradin wani abu ga
wanan takardan ga numbe waya ki kira ki zabi
dayadaga nau'in abincin da kike so ko na sha, za
a kawo miki.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta
Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-
Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_
ID10%2C737012347
Har ya kai bakin kofa sai kuma ya dawo, ya ciro
wallet dinsa ya bude ya ciro katin MTN ya miko
min.Gashi ki loda a wayarki.Ya sake juyawa ya
tafi, tare da cewa ki kulle kofar in yazo zai
kwankwasa sai ki bude, na barki lafiya.A sanyaye
na ce, na gode.Tunda ya fita ta gumi na hada,
tunani da zullumin abu biyu ne na farko in ya zo
mai zai faru?Sanan yaya zan kare da fada iya in
na komagida?Ban ma san takaimaimain lokacin
da zamu bar nan ba.Fim din da ake yine ya dan
shagaltar dani, don haka ban lura da lokaci ba,
sai da na kalli a gogo na rude, shida dai dai na
yamma.A raina na ce tafiya zanyi.....kwankwasa
kofar ya dakatar dani, na bude cike da faduwar
gaba, a zatona shine ashe ma aikacin gurin ne
yake tambayata ko zanci wani abu?Na ce a a yace
kada ki damu Oga ya na nan zuwa, ban tanka shi
ba na maida kofar na rufe.A raina nace wato har
sunsanshi tunda gashi suna cewa yana zuwa.Na
ce wa yasani ma ko yana zuwa da mata.....na
katse zancen da cewa a'u'zubillah, ba kyau
munmunan zato.mikewa nayi ina ta kai komo a
tsakar dakin, tunanina wa zan kira wanda
zaikaiwa iya waya in mata bayanin cewa yaya
nake jira mu dawo.Can na tuno da Bello, na kira
wayarsa dan akwi number shi a wayata, kuma
yana kiran Aisha itama tana kiranshi da layi
na.Muka gaisa, na ce dan Allah Bello in kana

kusa ina son magana da Aisha ne, tayaya zaka taimaka min?Ya ce bani minti hudu zuwa biyar a kai mata. Na ce nagode. Sai da na bari kusan minti shida sanan na kira cikin sa'a kuwa ta daga.Na ce,Aisha taimako nake nema a wajenki, don Allah.Ta ce na me?Na ce, kin sani ne?Mun fita har yanzu bamu dawo ba, shine nakeso kije kicewa iya don Allah kada taji shiru mun nan dawowa.Ta ce, keda wa kuka fita?Na turo baki tamkar ina gabanta, nace da wanan ya Aliyun mana.Da sauri ta ce, au, ke da mijinki kika fita? Bata jira amsa ba ta ci gaba da cewa, to ba zan fada mata ba, na zata ma ke da wata ce, to in shekara ma zakuyi ina ruwanta?Ta ja tsaki.Dan Allah malama in zakiba mijinki kulawa ki bashi kulawa kawai, sai an jima ta kashe batare da nasake jinta bakina ba, nayi sororo ina kallon wayar.Shi kuwa ya Aliyu daidai wanan lokacin ya isa gidansu iya.Tana girki yayi mata sannu da gida, ta ce yauwa ina yar tawa?Ya ce, yace yanxu zanje in sameta in nayi wanka daga gidan oga xuwa gidan sauran Abokai na.Murmushi iya tayi ta ci gaba da cewa, wai ni za'a yiwa wayo, nifa na haifesu, ni fa duk abinku kar nake kallonku. Shiri yayi ango sosai, sai zuba kamshi yake yi, ya nufi masauki na comman bayan yayi tsarabar kaji da lemuka da kalolin madara masu tsafta. Ya gaisa da masu tarbar bakin inda wani daya yake tabbatar masa da cewa a jiyarsa na nan a ciki, sun lura da ita yanda ya kamata.Kwankwasa kofar ta re da muryarsa naji, inda yake cewa Dear my choice.Jikina ya dauki bari, naje na bude kofar tare da yi masa sannu da zuwa.Na amshi ledojin hannunsa, kallo yake tayi tunda ya shigo har ya maida kofar ya rufe, na ajiye ledar na zauna kan kujerar dake kusa da gadon.Kai tsaye yazo ya zauna kan hannun kujerar.Dear my choice kinjini shiru ko?Yayi maganar cikin wata laulausar murya

Na kalli a gogo gabana ya ci gaba da faduwa, nace gashi har magariba ta karato, yanzu iya tana can aiki yayi mata yawa, tana kuma jira na.Ya kama hannuna me zakiyi mata da zata

jiraki?Na ce abincin dare mana.Ya hada tafin hannuna da nashi ya sarke.Sanan ya dan matsa, in kin tare a gidanki wane zai dinga yi mata aiki? Cikin raunaniyar murya na ce, zan ke aika mata duk abin da naci.Idanu na suka kawo ruwa don tunanin rabuwa da iya.Ya dago fiska menene na kuka?Na ce, ina tunanin rabuwa da iya ta ne.Ya kwantoni jikinsa.Yi hakuri kanwata, ai ba wani nisane tsakanin mu da iya ba, kullum nasan zatazo ta duba ki, in bata zoba kuma mu zamuje.Na kalli cikin idanunshi, da gaske zamuje? Ka min alkawari fa.Ya ce, in sha Allahu.Ya ciro fari kar din hankici mai kamshi daga aljihunsa ya soma share min hawaye.Tashi kiyi alwala muyi sallah sai muci abinci.Gurin da na idar da sallar ya sameni, ya bajekomai gani da shegen kwadayi, amma fargaba ya hana ni ci.Duk hankalina tashe yake, ya lura da haka, sai ya soma lallashi na.Haba Sadiya my coice, me nene naga duk kin damu?Nifa mijinkine na sunna.Nace, to ai iya ta ce kada wani abu ya faru tsakanin mu, har sai mun tare.Ya ce to zata sani ne, ko ke zaki fada mata?Na soma kuka, ina kallon fuskarshi.Wlh yaya zata gane.Zumbur ya mike daga kusa dani ranshi a bacce, ya soma yin magana cikin daga murya.Kina fakewa da Iya ne kurum dan kawai ki cucheni, ba fa haramun zan aikata ba.Kinsan ina kyalekine ina lallabaki, in nace zan gwada maki isa ba zaki iya kwatar kankiba ko?Jikina ya soma bari, yaya don Allah kayi hakuri.....Yi mun shiru.Ya katsane, sai wahala kike bani kina wani inyi hakuri, ba zan hakura ba, haka nan ba zan matsa maki ba, amma ki sani baki ba komawa gida ko da zamu shekara a nan harsai kin yardar min a bin da ya halasta min.Na fara kuka wiwi shi kuma ya fice ya zare makulli ya kulle ni ta baya.Na fada kan gado ina kuka, wata zuciya ta ce mun gara fa kiyarda dan sai kin dibi kunyar da bakiso a hannunki, don dan shi namiji babu ruwansa.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook

https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Dasauri na dauki wayata na soma kiran layin sa.Tayi ringing kusan sau biyar sanan ya daga, cikin kuka na ce, yaya dan Allah kazo na yarda....Da zafin rai ya ce, bana so, ke har kin isa mzacen da zaki ja raina?Bari kiji wani abu, baki son ki dade kada iya ta zargeki ko?To ina mai shaida maki cewa nan zaki kwana, in yaso in kin koma gida sai inga maizai faru.Ya kashe wayar, ransa ya baci dani sosai.Daya wayarsa ta soma ruri da sauri ya cirota don in yaji ringingi din ta daga office ne, duk da ba ganinsa yake ba sai da ya nutsu da ya daga ya ji muryar.Cikin sauri sauri yake magana.ASP kana ina ne?Aliyu ya ce, ina nan kan titin waff Road.Ya ce, yauwa kana kusa ma, yi hanzari ka iso nan (headquarter) ka kwashi yara ku nufiunguwar rimi layin dan marina gida mai lamba tara, yan fashi sun shiga gidan sunyi fashi.Sanan sunyi gaba da babban yaron mai gidan.Ga ni nan zuwa ranka ya dade.Aliyu ya amsa cikin izza, a duk lokacin da aiki ya taso Aliyu yakan mance da duk lamarin dake gaban sa matsawar ba salla ba ce.Sun isa gidan da yan fashin suka shiga, Aliyu tare da inspector Adamu da sajan Musa, sai kofur Bala.Cikin natsuwa Aliyu ke kallon ko ina, kafin ya soma magana.Hajiya sannunku da juyayi.Ta ce, yauwa.Cikin kuka da rawar murya ta amsa, ya ce ina mai gidanki?Ta ce, baya nan, kuma dama sunce shi sukazo nema.Ya kalli kofur wanda tuni ya soma rubuta komai, ya sake maida kanshi ga Hajiyar.Ta ina suka shigo?Ta ja majina, sanan ta ce ta kofa.Ta ci gaba, sun ga Yusuf ya shigo a cikin motar baban su to sunyi tsammanin shine tunda gilashin mai duhu ne.Don haka sai suka biyo shi.Aliyu ya ce, shi Yusuf din daga ina yake?Ta ce, daga masalaci ya ke, babansu yayi masa waya, cewa yaje ya dauko motarsa.Don ni ya soma kira wai in kira masa Yusuf ya dauki motar, sai na ce ya kira layin sa ya fita masallaci.Kuma ba lallai bane daga can ya dawo gida ba, Aliyu ya gyada kai

alamun gamsuwa sanan ya ce, motar ta samu matsala ne?Ta ce, a a.Sau biyu ana biyo shi ana kai masa hari a motar da dare shi ne dalilin da yasa sam bayason karfe tara tayi masa a motar na dare.Yau ma mitin ne zasuyi da ya taso musu da gaggawa kuma bai san lokacin da zasu tashi ba.Aliyu yayi taku zuwa tagar ya daga labulen windon yana kallon harabar gidan haskenta kamar duhun magariba baiyi ba.Ya waiwayo ya dubeta wace mota ce daga cikin wayan nan motocin guda uku?Ta karaso ta daga dayan labulen windon wanacan (hondar ce) baka CRV.Ya saki labulen yanzu mai gidan ya sani?Ta ce, a a yana kashe duk wayoyin shi ne in zasuyi mitin.Ina ne gurin aikin nashi?Aliyu ya bukata cikin rawar murya ta ce, shine manaja a first bank.
Aliyu yayi shiru kamar mai wani nazari, can ya ce zaki iya fada mun kamannin yan fashin?Ta ce, eh, zan iya.Babban su baki ne dogo kuma kamar yanada yare, don hausarshi bata goge ba.Sai dai kila muslmi ne, sauran kuma biyu fararene ina zaton fulanine, biyun dake waje ne ban tantance su ba.Aliyu ya jefeta da wata tambayar, yaya kika yi tsammanin musulmine? Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ta ce, haka kawai naga kamar musulmine.Aliyu yayi guntun murmushi.Bari mu barki haka, yanxu bari muje mu dora bincike.Ta sake fashewa da kuka.Ran ka ya dade ka taimake ni yanzu yaya za'ayi mijina ya samu labari dan kada ya fito sukama shi?Aliyu ya ce, kada ki damu, zamu bashi kulawa da tsaro, sanan ki saurara sosai nasan zasu kiraki ina zaton garkuwa zasuyi dashi.Kiyi mana saving din number, in kuma ba number ki kiramu ki sanar da mu.Ta ce, to yallabai na gode.Ya ce ba komai kiyi adu'a.Suna fita ya kira AC ya koro masa komai, AC ya ce, to

yanxu ku fara ji da maigidan nata, sanan kunsan yanda zakuyi ko?Aliyu ya ce, yes Sir!Sai dai ina kake ganin za a bashi mafaka tunda ba dama mu barshi ya koma gidansa?AC ya ce kuxo nan dashi daga nan sai a kaishi inda ya dace.Aliyu ya kara cewa yes sir.Ya dubi yaran kumaje first bank.Sha biyu da minti ashirin, Alhaji auwal ya fitoa rikice daga cikin banki, gama mitin dinsu ke da wuya police commissioner ya kira shi bayan ya kunna wayarshi.Ya fada mashi cewa ga yarana nan zasu taho dashi dan kare lafiyarsa.Alhaji auwal ya ce saboda me ranka ya dade?Commissioner ya ce, masu bibiyara ne suka shiga gidanka, amma ka kwantar da hankalinka za a kama su.Suna tafe cikin mota Alhji sai adu'a yake yi yana tunanin me ya tarewa wadan nan bayin Allah?Kofur ya ce, Alh kaji cewa sun tafi da yaronka?Aliyu yayi mashi tsawa da cewa kofur?Da sauri kofur yace yes sorry sir.Alhaji Auwal ya ce ranka ya dade wane dan nawa dauka Yusuf? Aliyu ya ce kada ka damu, in mun isa can zakaji komai a bakin yallabai, kuma duk abubuwan zasuxo da sauki. Alh. Auwal ya ci gaba da adu'a.
Ofishin commissioner yayi tsit tamkar babu mutane sai karan (ac) da na fanka.CP ya kalli Aliyu dake kame, ya ce nasan kana da kwazo Alhamdulillahi,yanzu sashin binciken mu na takama da kai.Domin aikinka kanayinsa da karsashi gami da izza.Ya kalli Alh. Auwal kada ka damu Alh, babu abin da zai samu yaronka.Zamu baka kula shi kuma zamuyi dauki badadi da su.Alh, ya ce, kana ganin ba zasu kashe shi ba? CP ya ce, ai kudi zasu nema munsan irinsu, sai dai yanda tayi kwatancen shi ina zaton bako ne kila kuma ya jima yana yi bamu taba arba dasu ba ne.Amma wanan karon in sha Allah za mu hadu.Ya kali Aliyu ASP aje ayi shiri yanda ya kamata.Ina bukatar barayin nan tako wane hali sai dai banda kisa zan saurari wayarka a ko wane lokaci kwa iya tafiya
Sai da Aliyu ya tunkari gida sanan ya tuno da wata Sadiya, amma duk da haka bai wani damu ba dan yasan zata sami kulawa yan da ya

kamata.Ya sake ciro waya ya kira, jim kadan aka daga, ya ce Ibrahim dan Allah ajiyata na nan?Aiki ya rike ni da safe zan turo aboki na ya tafi da ita.Ibrahim ya ce ba ko mai yalla bai.Sun saba da Ibrahim ne sakamakon wata matsala da ta taba tasowa a Hotel din su Aliyu suka bincika case din.Ibrahim shine me kula da dakunan kwana na cikin Hotel din.Motar yansanda tayi faking a kofar gidansu Aliyu ya shiga gidan da hanzari.Sai da ya gama shirinsa sosai sanan ya nufi dakin iya.Tana kokarin fitowa suka ci karo, yace iya na kama hanya zantafi wajenta aiki ya taso.Usman zai tafi ya daukota ko da gobe ne.Kar ki damu canma gida ne gidan Oga ne.Haushi ya hanata magana, Aliyu ya dafa kafarta, ki min adu'a iya da yan fashi zamuyi arta bu, kin san aikin mu bakin rai muke yin shi.Ta ce Allah ya baku sa'a.Gudu gudu ya fito.Da kallo ta bishi har ga Allah bana son aikin dan sanda amma bata so ta bata rai a kan haka, dan kada ta tauye shi.Ta tabbata adu'ar ta ita ce daukakarshi, fushinta zai iya tauye shi a fili ta furta, Allah ka yi wa yaran nan Albarka dukansu, ka dorasu a kan hanya ma daidaiciya amin.Nikam a a lokacin ina can tsoro, fargaba da bakin ciki sun isheni.Kai har da nadama.Naji haushin kaina da naki bin umurnin mijina, gashi yanzu ya tafi yana fushi dani.Nasan mala'iku ma ba zasu raga min ba, kuma iyar da nake cewa zata yi mun fada in taga na dade, to sai dai ta kashe ni.Dan ina ganin tabbas nan zan kwana.Da na bi umurninsa kila da yanxu mun tafi gida cikin jin dadi.Kila ma yayi ta shi min albarka, mala'ku suna amsawa.Naja tsaki tare da cewa, kash! Nima ban yi ba wlh.Haka nayi kwanan zaune, danma na rage daren da yin nafilfili, sai da nayi sallar asubahi sanan na kwanta.Bacci ya tafi dani, ban farka ba sai kusan sha daya.Kwankwasa kofa ne ya tasheni, nazo na ce wanene?Ya ce, Ibrahim ne.Na ce, ai ya rufe dakin ya tafi da makullin.Ya ce, ba ko mai ga wani makullin, me kike bukata? Nace ba ko mai, akwai abinci a nan dakin dayazo dashi jiya.Ibrahim ya ce, to shi kenan.Ina jin takun tafiyar sa, na zauna a gurin dantsabar

takaici, bani da ma ranar tafiya gida ke nan.Shi kam dai dai wanan lokacin yana gidan Alhaji Auwal cikin falonsu inda yake sauraron bayani daga bakin Hajiya.Yanda sukayi da yan fashin da suka kirata.Ta ce, kamar yanda kayi zaton zasu kira sunkira ni yau ya da safe.Aliyu ya ce, karfe nawa?Ta ce takwas da rabi dai dai suka ce kudi suke so naira miliyan uku da rabi.Sun ce in har ba a sami kudin ba zuwa jibi zasu kashe shi, kuma sun ce basa son jami'an tsaro su shigo ciki, kuma basa so a nemi ragi.Me kika ce musu?Ta ce, ni kuma duk abin da suka ce da to nake ta amsa musu. Ya gyara zama ya ce, ina suka ce a kai musu kudin?Wai filin golf.Ina number da suka kiraki?Ta dauko wayar ta fito da namber ga ta nan.

Ya amsa ya dauki number sanan ya fita harabar gidan yana sanar da CP halin da ake ciki.CP ya ce, ka tafi da layin kamfanin su, wane layi ne? Aliyu ya ce (MTN) ne.CP ya ce, maza ka tafi dashi ka tambatar kayi abin da ya dace da wuri, dan kila cire layin zasuyi ko kuma anjima su kira da wani layin da ban.Aliyu ya ce, an gama sir.Sai da yaje office din Usman sanan ya tuna da Sadiya.Bayan sun gama magana akan abin da ya kai shi, dama usman MTN yake aiki, sanan ya ce, wanan yarinyar mai shegen tsoron tsiya, kuka tayi ta min na barta na tafi abina.Idan ka tashi dan Allah katafi ka taho da ita don ni ko ganinta bana son yi.Usman yayi murmushi, sanan ya ce, kayi mata uzuri, kasan yarinya ce sai a hankali.Usman ba da bata lokaci ba ya sanar da manajan su, nan take aka soma gudanar da bincike a kan lambar.Sun gano layin a yanzu baya kan waya, amma sun hada komai yadda da an dora shikan waya zasu gano inda mai layin yake.Nan take kuma ya kira CP yayi masa bayani.CP ya ce, good! Kara zage damtse in kuma kana bukatar yara duk sanar dani.Yes sir!Inji Aliyu.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook

https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Na idar da sallah azahar ke nan sai naji alamun ana bude kofa, fatana Allah yasa yaya Aliyu ne, in sha Allahu yanzu nan zan bashi mamaki
Sai dai kashi!Ya na budewa sai naga yaya Usman, ya ce tattaro kayanki muje gida.Na dauki jakata da mayafi, sanan na gaishe shi, ya amsa tare da cewa ki kwaso lemukanmana.Na ce, na kishi da su. Ya ce, ai kya kai wa iya tsara ba ko kina nufin gidan Oga ba a baki ko mai ba duk da cewa kin kwana?
Yayi tambayar cikin zolaya, na dawo na dauka, har ya taya ni sai lokacin naga Ibrahim din da suke nagana, gajere ne baki.Sai da muka tsaya Marhaba Store ya kara min tsaraba wai harda turmin zani matar Oga ta ce a ba Iya.Da zan fita nace masa nagode, ya gai da anty Abida, ya ce zata ji.Sanan ya ce, ki saki jikinki don kada ta gane ba can kika je ba.Ina yin sallama iya tana zaune, cikin faduwar gaba na isa gurinta ina yi mata sannu, ta amsa fiska daure.Jikina yayi sanyi, nayi karfin halin cewa.Iya kin ganni sai yanzun?Tun da yaya ya kaini ya Aliyu bai zo ba har sai da na kwana, wai suna aikin wani case ne a hannun sa.Iya ta ce, kai ma dallah da jin haka sai nayi shiru, don na san zance na bai shiga Iya ba, na mika mata leda.Gashi inji matar ogan yaya din wai in baki tana gaida ke.Sai naga iya tayi murmushi ta girgiza kai, sanan ta ce an gode.Tun lokacin ban sami bakin magana ba sai daki da na shige na kwanta.Har yanzu haushin kaina nake ji, da na sani nabi umirnin miji na, gashi wanda naki don ita bata yarda ba, kuma nayi imani ko da mezan ran tse ba zata yarda da ni ba.Aliyu yayi nasarar kama dan fashin nan tare da taimakon masu layikan wato network na waya.Don yan fashin sunyi anfani da layika dabandaban, ya kama oga tare da wani yaronsa guda daya, jim kadan bayan an basu kudi sun saki yaron.Sun dauki hanyar kawo da a lamun zasu bar Kaduna ne, ya harbi tayarsu sanan ya

harbi ogan a kafa.Sauran sun gudu shi kuma dayan tsayawar da yayi zai dauki kudin daga but din motar shi ya kawo Aliyu yayi nasarar kama shi.Wanan gaggarumar nasarar ta sa an karawa Aliyu girma daga ASP zuwa DSP, inda aka tara yan jaridu suka watsawa duniya.
Duk kwanakin nan da aka dauka sam Aliyu baya shiga harka ta, in na gaida shi zai amsa amma ko kallo ban isheshi ba.Haka nan har daki na same shi don inyi masa murna kan karin girman da ya samu, amma sai ya ce dan Allah in fitar masa daga daki.Har Iya ta na ce mun Allah ya kara, tun da na ba da kaina ba loka cin da ya da ce ba ai yazama dole in jure wulakanci, bani da hujjar yin musu dole in yi shiru.Gadan gadan ya tada aikin gidan sa, da alamu ya sami kudi, ranar wata a Abar bai fita da wuri ba.Sai da suka shirya sanan sun fita hanya sanan ta soma yi masa fada me yasa yake yiwa marainiyar haka?Ya ce, bata jin magana ne, gara ma ki mata fada tun yanxun don ba zan dauki gaddama ba.Sunje iya nata santin gidan, ta ce gobe kawo kayanta ko?Aliyu ya ce, amma na dakin anjima zan kwasosu har da TV da su Radiyo, kema na sai miki TV.Ta rinka godiya.Washegari makota da yan uwa tare da matan yayan mu sukazo suka yi mun jere, da dddare kuma aka yi mun rakiya.Iya tayi mun fada sosai, kuma ta kara nanata mun cewa tunda ni na dage da son ya Aliyu lallai in lallaba halayanshi.Don bata so in kawo mata wani kara'i sananta sa mana Albarka tare da yi mana adu'a tagari.Kowa ya tafi sai ni daya, nayi sallar isha'i da shafa'i da wutiri, sanan nayi wanka, kwalliya sosai nayi duk da cewa ina cike da fargaba zai kalleni ko ba zai kalle ni ba.In ma ya kalleni ni me zai faru?Goma da wani abu naji ana kwankwasa kofar gidanmu.Da sauri naje na bude, shi daya ne kuma sanye da kakinsa na dan sanda, ke nan shi Abokanai ba zasu rakosa ba kamar kowane ango.Na amshi kayan hannunsa, jakace da leda tare da yi masa sannu da zuwa, ban zaci zai amsa ba, amma ga mamakina najini a jikinshi ya rumgumeni tsam.Sanan ya amsa da

yauwa sannu.Ina makale a kafadar shi ya kulle gidan mu.Ina mamakin halin yayan mu sosai, tamkar bashine yake gaba dni ba.Abaki yayi ta bani kazar da ya shigo da ita tare da madarar holandia.Duk fargaba ya cika ni, amma haka naita sha har sai da yaga kamar zanyi amai, ya ce, kin koshi?Na ce eh.Munyi Sallah inda ya dafa kaina yayi mun addu'a.Bai bata lokaci ba gurin ibadar aure, wasanninsa sunyi mun nauyi.Don haka na soma rokonsa yayi hakuri, mai makon haka sai yaji kamar wata sarewa nake busa mashi.Nasha wahala a wanan daren nawa na farko, domin duk wani haushinsa sai da ya huce shi, sanan ya dawo yana tausaya min.Don shi da kanshi bai sai saita kanshi ba.Shi ya taima ka min na gyara kaina.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ba mu jima da kwanciya ba aka kira sallah, ya tafi masallaci nima nayi tawa sallar.Naso kwanciya amma sanin cewa zai fita da wuri yasa ni shiga kincin don hada abin kari.Lokacin da ya dawo zatonsa zai sameni a kwance, sai ya ganni kicin.Ji kawai nayi an rumgumeni ta baya.Na gaida shi ya amsa ya ce, naje nayi bacci don yasan ina jin bacci, na ce ba komai inya fita zan kwanta.Tare muka karya, sanan ya ce, inzo in cuda masa bayan sa tun ina jin kunya har na gyare don kuma yariga ya tsomani cikin ruwan.Tundaga ranar komai tare muke yi, wata masifafiyar soyaya yake nuna min har na dinga mamaki, sai dai ina gyaruwa wajen kwanciya.Don ya Aliyu mabukaci ne fiye da zatona, rana, safe, dare office ma sai ya dawo, haka nayi ta jurewa, saboda yana ririta ni kamar ya hadiye ni.Satin mu biyu nayi fari fiye da da, fatata ta goge, amma na rame.Dan Almajirin da ya so min shine ke min aike, kullun sai na saka mai abinda muka ci ya kai ma iya.Ranar da nacika sati biyu ranar

iya tazo, dukinda nayi iya tana da ido, bayan na bata ruwa da abin tabawa sai na zauna kusa da ita ina cewa iya nayi kewarki sosai ke fa?Ta ce, Sadiya kewa ai ba a magana.Amman kuna zaune lafiya?Na ce lafiya lau, Iya.Yaya na ji dani, baki gani ba.Tace Sadiya ni sai naga kin rame, kina cin abinci kuwa?Na ce, ina ci mana.Aka kwankwasa gidan, na ce gashi nan ma.Da sauri naje na bude, ya manneni a jikin sa na ce iya tazo.Ya ce tana nan?Na ce eh.A zatona zai sake ni amma har fallon mu saida ya zauna sanan na zame na barsu suna gaisawa da Iya.Na kawo masa ruwa da abinci, yace my choice ba zan ci abinci ba, dama nazo ne in dubaki kawai don na kira wayarki a kashe.Nace yanzu aka kawo wuta, ka kuma san batir din baya rike chaji.Ya ce, haka ne.Zan chanja maki wayar ma, Iya ma in sai mata.Tace ni yanzu gadanga in ka hada ni da waya ban san yaya zanyi da ita ba.Na ce, zaki iya mana, mun gode yaya.Yayi murmushi tunkafin a siyo?Ta ce, ai nasan tunda ka furta zaka aikata.Iya ta ce, gadanga kai naga kayi bul ka kara kiba ita ko yar tawa duk ta rame.Ya kalleni, ashe bani kadai nake ganin wanan ramar ba, to ko Asibiti zamuje?Na ce, yaya babu inda yake min ciwo sai muje Asibiti?Yace rama ciwo ne My choice, zasu baki magani.Iya ta ce, ni da na zaci ko rigima kuke.Ya ce, haba dai, ai yar taki tana da biyayya.Iya tayi murmushi sanan ta ce, haka nike so,Allah yayi muku albarka, ya baku yaya na gari.Yaya ne, ya amsa da amin.Tare da dago haba ta.Iya ta ce bari na tafi.Naje daki na dauko dubu daya na ce, iya gashi, ta ce ina kika sami kudi?Na ce, in abokan yaya suka zo suka bani, ko na bashi sai ya ce in ajiye abina.Kuma ni ko katin waya shi ke loda min.Ta amsa tare da ce min Allah ya anfana.Na ce, Iya da kin dan bari sai anjima.Yaya ya harareni ke zakiyi mata aikinta a gida?Na ce, (cikin shagwaba) ba ina kai mata kullum ba, ia yana isarki ko?Ta ce har ma in rage in ba wani.Sai dai duk da haka ina yin girkin saboda almajirai ko yan ciranin nan na mokatanmu.Na ce, har yanzu iya kina ci dasu?Iya

ta ce, wanda ka bada shine naka.Nace to ki tsaya zanyi da yawa sai in sa miki.Aliyu ya kawo hannu ya dan mintsineni gefen ciki na, tare da cewa sauran aikin ke zakiyi mata?Iya ta nufi hanyar fita tana fadin Sadiyayyena kina in zauna shiko gadanga korata ma yake.Da sauri kuma cikin dariya ya ce, Iah, iya bankoreki ba, nima yanxu zanfita nazo duba ta ne kawai, kuyi zamanku ni bari na tafi. Duk muka sa dariya, Iya ta ce a a yayan nan ni dai naji dadin yanda na sameku haka, fatana Allah ya kauda shedan tsakanin ku.Ta bude kofar gidan ta fita, ya bita nikuma nayi mata alkawarin xuwa inyini in an kwanabiyu.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Bayan ya dawo daga yi mata rakiya ya sameni ina gyara gurin, ya makaloni jikinsa ya dago fiskata.Sarai kinsan abinda ya kawoni, shine kike rokon iya ta zauna ko?Gaba na ya fadi, amma sai nayi yake tare dafadin ba haka bane.Muka nufi dakinsa.Na rasa duk lokacin da yaya zai zo mun da wanan batun gabana ya dinga faduwa kenan.Na kasa sabawa.Ko shi ke sani rama?
Oho.Kawaye na duk wace tazo sai tayi zancen ramata, haka Aisha, ta damu da son jin dalili
Na dage kan cewa ba ko mai, tunda bai kyautu in fada mata yanayin mijina ba.Munje Asibiti likita shima ya sha mamakin jin banda matsala kuma ba inda yake min ciwo, amma na rame.Sai dai ya ruvuta mana magunguna masu sa cin abinci, amma duk da haka sai a hankali.Wani dare anty Abida ita da Usman sun kawo mana ziyara munata hira, sai Aliyu ya kawo batun ramata, aka danyi zancen har Usman yana tsokanata da cewa ina tsoron kishiya ne ki daina tunani, aboki na naki ne ke daya.Nayi dariya sanan na ce, nasan haka shima yasan haka.Yaya Aliyu yayi dariya.My choice ban maki alkawari ba fa.Na ce, yaya kaima

kasan ko bakai min alkawari ba kai nawa ne ni daya.Abida taja ni bed Room dina muka zauna bakin gado, ta kalleni wai me yake damunki? Na ce, ba ko mai wlh.Ta ce, ki fada mun ban sani ba ko zan iya taimakonki.Nayi shiru ina nazari, can nace anty ba ko mai, Allah sai dai ina zaton ko dan yaya yana da yawan buka ta ne?Kin san Allah anty na yaya bashi da hakuri hatta kai da na ganshi ya dawo gaba na ya dinga faduwa ke nan.Ta kada kai zancen ke nan, amma wanan ba abin damuwa bane, da farko ki daina tsorata har gabanki ya dinga faduwa.Kisa haka aikin da ya zaman maki dole, aure bauta ne, in zakiyi sallah gabanki na faduwa?Na ce, a a.Ta ce aikin gida fa? Na ce, a a.Ta ce, wanan ma kisashi cikin dolenki, tunda zama ne ba na kare ba.Gashi baki son kishiya.Tayi dariya sai dai zan fada maki wasu abubuwa da zasu taimakeki, dauko biro da takarda.Na ce, to.Na tashi na dauko memo, ta soma bayani kamar haka:
ki samo Dabino,Zuma,Aya, da Cukui zaki maidasu gari ne, sanan ki dinga zuba madara peak da zuma kina sha kullum safe da yamma.Kinji daya? Na ce eh, na rubuta.Ta ci gaba, ki samu,kankana ki dinga yawan shanta har kwallon,na ce gashi kankana bata dame ni ba, ta zaro ido to kuwa ta dame ki, kuma kya iya yanyankata ki zuba mata madara peak ki dinga sha shima har kwallo.Sanan a kai na kan Akuya, ki dafa shi da romo, sai dai bazaki zuba mashi mai ba, maimakon mai ridi zaki zuba da yawa ki cinye ke daya.Haka kuma zaki sami garin dabino ki fasa kwai da madara peak ki juya ki shanye.Nace wai zan iya duk wanan?Ta ce, ki gwada tun gobe zaki sanya ya nemo maki amma karki fada masa dalilinki na son kayan, kawai kice zakiyi anfani da su ne.
Kan batun ramarki kuwa, ki canza abin kari, da me kike karyawa?Na ce,Tea ne sai Bread da Kwai, watarana inyi kunu da kosai, ko indomie da kwai.Ta ce ki koma cin dankalin turawa da agada,ko doya da kuma kwai, in da hali harda farfesu.Shayinki kuma ya zama yaji sugar da

bota, milo da madara.Ki zuba sosai yayi kauri kisha.Sanan kirinka baccin rana shima baccin yana sa kiba, sanan da daddare kici abinci sosai.Na ce, to anty na gode.Ta ce, ba komai, ke dai kada kiyi wasa, in kinyi su da kyau na tabbata sai kin dawo neman wasu.Ko da yake ban fada maki na tafin hannu ba,kin san hannu yana daya daga cikin mai aikawa da sakonni.In mijinki mai yawan kama maki hannu ne, ki samu zautun ki kwaba da suga ta narke, kullun in zaki kwanta ki rinka shafe hannunki.Sanan ki rinka shafawa a lebunanki, nace to na gode anty sosai.Sallamar yaya ce ta katse mu, ya ce, me ta baki kike ta godiya?Nace abubuwan karin kiba ne wanda zan rinka karin kumallo da su.Ya kalli Abida dama zaki iya wanan taimakon amma kika share mu? Muka sa dariya harda shi.Ya ce, mun gode.Ta ce, ba wani abu bane wanan har da za ayi mun godiya.Kai dai ka dage da siyo wa.Ya ce, in sha Allahu ko su ke nan kudin za a siya, me nene da me nene za a siya?Na ce, na rubuta zan nuna maka.Yayi murmushi, to da kyau, yace kizo, abiki yace zaku biya ta gidan yar uwarki ko?Ta ce, eh, tare da mikewa na shiga dube duben me zan bata, turare na bata mai kyaunace ta kaiwa Ummulkhairi.Ka fin ya dawo da ga rakasu, har na gama rubuta abinda ta ce na rinka karyawa da shi,ya ce agada da dankali sai da safe, nayi godiya da cewa Allah ya kaimu.Cikin satyn na hada duk wani abu da anty Abida ta fada mun, na shiga anfani da su.Kafin wata daya naga canji sosai, yanzu bana wahala da duk dawainiyar da miji na yazo mun da ita.Sanan nasoma cika ina cika kayana gwanin sha'awa.Shi kanshi yaya wani sabon ji dani ya sake ko mai tare muke yi in har yana gida ni dashi mun zama abu daya.Ko tari nayi sai ya tabbatar ba na cutarwa bane, haka nima ina binshi sau da kafa, da ya nuna ra'ayin abu zan masa balle ya ce my choice ina son kaza.Ai in na soma sai ya gundire shi, duk abinda bai so na kiyayeshi har abada.Shinfidar da muka yiwa rayuwar mu ba zan iya bada labarinta ba, kowa yana mamakin mu tamkar mun shafe

shekaru goma muna soyayya kafin muyi aure.Muna cikin wata na uku iya ta matsa masa wai sai ya maidani makaranta, form din (N.C.E) ya sai min bada bata lokaci ba na zama daliba a makarantar horas da malamai dake riga cikun.Aliyu ya ce, ya zama dole in nemi avin hawa ko don ke.Na ce Allah ya bada iko.Ba da jimawa ba kuwa ya ,mallaki motarsa dai dai ta talaka.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Don haka bani da matsala sai dai yanayin aikin sa ya ce in ya sami lokaci zai rinka koya mun, na ce to.Ban jima ba na iya mota, sau da yawa ni ke kaishi gurin aiki in dawo, sanan in tafi makaranta.Kai yaya ya nuna mun dukkan gata, a lokacin jini ke babu matar da ta kaini sa'ar zuwa duniya a zamaninnmu. Wata safiya na farka da zazzabi, mura, ciwon kai da sauran su, gashi ranar yaya ba gida ya kwana ba, saboda wani case da ke hannunsa.Bana kiranshi in dai yana wurin aiki, amma shi in ya sami lokaci yana kira na.Ina kudindine a kan gado naji ringing waya ta, da kyar na lallaba na dauko, na daga.Ya ce, my choice kin wuni lafiya?Cikin wata murya na ce, lafiya lau.Ya ce, me ya same ki naji ki haka?Wani dan kukan shagwaba ya subuce mun na ce, zazzabi.Nanfa ya rikice sai gashi a gida bayan minti ashirin.Banyi ko wanka ba ya sani a mota sai asibiti, gwajin farko ciki ya bayyana, murnar da ya Aliyu ya dinga yi ta rinka bani mamaki.Kula da tarairaya ina ganinsu gurin sweet Aly na da iya, cikin ya sa ni yin kyau, duk da na sha wahala kafin yayi kwari.Sanan na bude nayi kiba gwanin sha'Awa.Lokacin da cikin ya tsufa sai kuma na kumbura abin da yayi matukar daga hankalin yaya.Duk da cewa likitan ya ce babu matsala.Cikin haka aka chanja yaya zuwa kogi, ranarda ya zo mun da maganar na sha kuka.Duk

da ya zaci dama zanyi rigima bai tsammaci har haka ba.Yayi ta lallashina da cewa, sadiya my choice,ki kwantar da hankalinki.Ai duk matar mai kaki San sanda ko Soja da sauransu, dole ta kwana da sanin akwai yawon zaga duniya.Banzaci zan dade haka ba tare da an canzani wani gari ba.Na shafa cikina yanzu baka nan zan haihu?In katafi yanzu sai yaushe zan sake ganinka?Ya ce da na sami sarari zanzo, na kwanta a jikinshi.Ni dai zanbika sweey Ali kaji yaya na?Ganin yanda na rikice sai ya ce, to shi ke nanmu tafi tare ko? Na ce, to sanan nayi shiru.Ana gobe zai tafi yaje suka hada baki da iya,na zage ina ta hada kaya har yana taya ni, sai ga iya tayi sallama.Na ce, sweet yaya na dubi iya tazo kamar tasan zamuje sallama.Iya ta shigo har cikin daki na, ta kalli kayan da akwatinan ta ce, wanan fa, kwalima ce? Na ce iya kin manta gobe ne fa zamu tafi can jihar kogi inda aka tura yaya.Iya ta ce, zakutafi ko zai tafi?Ina zaki tafi da wanan katon cikin ga kumburi?Na kalli yaya na wanda ke ta aikin jera min kaya na a cikin a kwati.Ni ina kwasowa daga cikin sif.Kin kallona yayi, sai da na ce yaya!Ya kalleni na ce, kaji kuma wai ba tare zamuba, inji iya?Ya ce, eh, a a ai kinji ta ce saboda cikinki na ce, tabdi jan!Ni kam ba zan zauna ba.Iya ta ce, lallai Sadiya ba inda zakije yar dadi muji, ni yanzu ma zuwa nayi in tafi dake.Na saka kuka, iya sororo tayi tana kallona, shi kuma sai ya tashi tsam ya dawo kusa dani.Iya kije gida zan kawo ta.Iya ta mike ai ba wani lallashi ba in zata zo dan ma kada ka sake yi mata karya.Ke ko yanxu ance ki bishi kya je?Na ci gaba da kuka na iya dai ta tafi tana cewa sai kiyi ta yi.Tana fita ya rungumeni, haba my choice ni na lura iya tafimu gaskiya.Ki bari in kin haihu sai muje, ina zo zan tafi dake.Yanzu kinga dole inje in ga yanayin garin.Na ce, yaya dama na san cewa baka damu dani ba, can na san baka sona.Ya manneni a jikinsa, inji wa yace bani sonki?A zaman da mukayi baki fahimci matsanancin son da nake maki ba?Na ce, to me yasa zaka tafi ka barni?Ya ce, ina canne amma na rantse maki zuciyata tana

tare dake.Yanxu ni dake bamu san haihuwa ba, gashi yanayin aikina ba na za,ma bane bugu da kari ba mu san kowa ba in haihuwa ta zo maki bana kusa yaya ke nan?Nayi shiru a raina na tabbata haka ne, amma damuwa ta daya, yaya na nasan ba zaka jure zama ba mace ba, don nasan yanayin ka.Ina tsoron matan zamani.Ya ce, au, dama dan wanan ne?Nayi maki alkawarin ba zan kalli wata ya mace da sunan so ko wani abu ba, baki tunabaya ba?Na tsare kaina kuma Allah ya tsareni, ba wanan a raina, nace to ya ya zakayi?Ya ce, azumi mana, ko can shi na tayi ta irin na annabi dauda.Inyi yau gobe in huta, kada ki damu ki kyautata min zato, bani da sha'awar aikata kazamin laifi irin su zina da makamantansu. Na kalleshi na yarda da kai mijina, kuma ni da kai mutuwa ce zata raba mu.Zan jira dawowarka, amma za ka dinga yawan kirana?Yace, kema na yarda ki kirani duk lokacin dakike so, nace to amma dai mu kwana abinmu a nan da safe in katafi sai na tafi nima.Ya ce, sammako zanyi, na ce, eh, duk da haka, ya ce shi kenan, sai muje da daddare mu kai kayanki ko?Na ce, eh.
Hakika yaya na sweet Ali ya tafi ya barni da tsananin kewarsa. Kafin ya kai munyi waya yafi sau goma.Haka nan na hakura na saba da kwana ni daya, daran wata lahadi na farka da wani matsanancin ciwon ciki da baya.Kafin in tashi iya yaya na soma kira, ya daga a rude na ce yaya zan mutu ka yafe mun, nayarda wayar saboda ciwon mara da ya murdo min.Kalamaina suka farkar da iya, tazo tana cewa haihuwar ce Sadiya? Yaya ya kashe ya sake kira a rude, iya ta daga ya ce Iya don Allah............Kuyimin hakuri indakata anan zuwa lokaci nagaba sai mudira daga inda muka tsaya,fatan zanga comment dinku rututu,kafin nan nake cewa zaku iya ziyartar blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_

ID10%2C737012347

Zaharaddeen Shomar
Whatsapp 08168575100

Darajar Yayana2-02
Posted by ANaM Dorayi on 09:51 PM, 02-Apr-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
__________________NA
____________HALIMA K/MASHI
Irin tarbar da kikayimin ta mutunci shi yasana boye kalatata,boye kishinki zaifi alheri, sama da bayyanashi don yanda na yi mani bakikaini son mijinki ba, haka na yi imani na fi ki kishin sa,in kina musu lokaci zai tabbatar miki dahaka. Kije kiyi aikinki sannan ki kunna min T.V Na harareta tare da jan tsaki na nufi dakin yaran. Sun gama cire kayan, Kausar tana linkewa, Al'ameen ya ce,'Mama wace ce wannan??? ..... Na ce 'Bakuwa ce, Na kunna musu T.V dinsu, na ce kar su fito sai an kira sallah. Nima na shige dakina na fada kan gado. Maganganun yarinyar sun ratsa ni, har na rasa tunanin dayakamata inyi. Ina buqatar shawara, domin na lura da 'yar iskar matar nan batazo dawasa ba. Wa zan kira don neman shawara? Aisha ko Abida? Aisha ba ta san d wannan zancen ba, bari kawai in kira Anty Abida tunda ta san da matsalar. Ringing na uku ta dauka na ce, 'Anty Abida ya gida da yara. 'Ta ce, Lafiya lau. Na kwashe komai na fada mata, ta cika da mamaki, sannan ta ce, 'Shawarar da zan ba kikar ki bari ta gane lagon ki kar ki nuna fushinki, kuma kar ki kulata kuyi tashin hankali, ballantana ta yi furucin da yaranki za su gane,ki jira zuwan shi muji hukuncin da zai yanke. Na ce, 'To shi kenan Allah yayi mana jagora.'Ameen, Ta ce. Na kashe wayar ina nazarin maganganunta. Ita ko 'Yar Gwari, Mujidat tuni ta ciro wayarta ta soma chatting da abokanta. Murfat ke

tambayarta wai yanzuntana ina? Mujidat ta ce tana Kaduna. Murfat tace, 'Ashe muna kusa ni ina Abuja jiya muka zo tare d Alhaji Karimu zai yi meetina na kwana biyu.. Mujidt tace lallai kina cikin kudi, murfat tace sosai ma, abokinshi Alh muslimu ya tambayeki .Mujidat tace yakiranima bandaga wayar ba, kinsan ina ina yanxu? Murfat tace ba kin ce kaduna b? Mujidat tace ina gidan officer Aliyu,Murfat tace kina hauka ne? Zaki je gidansa? sai matar sa ta kasheki a banxa? Mujidat tace ai matar tashi wawiya ce, har ruwa ta bani nasha, bayan na gaya mata cewa mijinta ciki ya min, tace ina baki shawara ki cire cikin nan kixo gurin masu sanki, officer ba sanki yake ba. Mujidat tace , ni inasonshi, zan tsaya nai fada a kanshi, saboda ko nadawo zanta tunanin shine, bazaki fahimta bane saboda bakitaba shiga tarkon So ba, ni kuma na shiga tarkon So mai tsanani.Murfat tace to yaya akayi kika gane gidan?ina kwance Hotel ba lafiya , sai ga wayar direban shi wai Ogafa an canxa shi zuwa Abuja, yanxun haka ya tafi in gaya miki duk sai na rude, take na miqe ina roqon Adewale ya taimakeni , yace sai nabashi kudi, bani da kudi sai dana roki samarina , suma shegu ban samuba sai dana musu alqawarin basu kaina, ina bashi kudin yace naje kaduna zai turo wani dan sanda daga can Headqurter su, yayi Tanbaya kan Aliyu Tukur aka fada masa sunan unguwar su, sannan na nufo Kaduna, nasha wahala kafin na iso, sabida motar dana shiga me arhace, inazuwanan na samu wani dan sanda da Adewale ya hadamu , shima akwai kudin da akayi alqawarin xan bashi, sai daya dafe shi,sannan yayi min jagora zuwa unguwar su Aliyu, nan ya bar ni wai in nemi gidan, wai in mun shig unguwar tare, asirinsa zai tonu, na Adewale ma haka,nadade ina yawo, sannan na samu gidan mamanshi, na shiga bata nan, sai nace a kai ni gidan matarshi, Murfat tace ke yar neman bala'i ce, bari tasa miki guba a abinci kici ki mutu, mujidat tace shi yasa bazan taba cin abincita ba,Murfat tace kidai yi ahankali, garinsu kikazo, tace a garinnasu sai in karbe mijin kuma

na zauna lafiya.haka suka yita chat har xwa wani lokaci, Niko munyi sallar magariba har na zubawa yara abinci, 9 da yan mintina yya Aliyu ya iso gida,da ita ya soma cin karo a falo, ckin zafin rai yace me zakiyi agidana?itam cikin daga murya tace goyon cikin dakayi min, abinda naji kenan, na miqe ina kallon yarana,Kausar ce kawai idanta biyu tana yin homework dinta, na miqe na fito da sauri, dai-dai lokacin yana cewa, zan nuna miki kurenki na biyoni gidana yar iska karuwa.nakamashi ina fadin yaya yara fa? itama tace yan iska dai, namijin karuwa. na dafa kaina dan takaici, yar bariki tana zagin mijina da nake girmamawa a gabana, najashi zuwa dakinsa, nace, haba yaya, kamanta cewa kana da yara a gidan nan?dubi yanda yar bariki tazo har cikin gidanka tana zaginka?sabida mutuncinka daka sai da,ai dama haka ne, dukwanda yabar maganar ubangijinsa dole ya fadawa dana sani, da wace rana zaka iya hada yau a gurinka dan bakin ciki? ni dai a gurina babu, ya dago kai ya dubeni, Sadiya nayi nadama sosai wallahi, ba sai ta kanjamau kadai Allah yake kama mazinaciba, in Iya taji batunnan na shiga uku, nasan bazan kara yin daraja ba, kila ma ta cireni daga yayanta, ga wannan matsiyaciyar da alamu fallasa tazi min,nace to yanzu dai nema mata masaukin da zata kwana, in yaso da safe sai mu zauna da ita mu kafa mata sharuda,ya kama hannuna, wadanne irin sharuda za'a kafa mata?kara min haske, sai musa mata sharudan cewa ka yarda zaka amshi dan,amma za'a rufa asirin cewa ba'a son kowa ya ji, dan haka za'a ce mijinta ne ya rasu, iyaynta suka koreta saboda ta musuluntam,na tabbata duk wanda yaji haka zai tausaya,to inta haihu sai ta bamu yaron ta tafi abinta,yace wazai rike yaron?nace ni mana, Yya ko ban aure ka ba ai xan rike maka da, bare kuma ina matarka na kasa rike jininka? yadan yi shiru yana nazarin batuna , can yayi dariyar yake yace,Sadiya baki tunanin me mutane zasu ce?in sun gammu da jariri?me zamu fadawa yaran mu? idan sun tambayemu nan gaba? nace ai zamu

fada musu dan mu ne, amma bani na haifeshi ba, tunda dama a musulunci bai da gadonka,kaga ba zamu sami matsala ba, ya sake yin shiru, can yace ina ganin fadin gaskiya kawai shine mafita, saboda duk rintsi karya bata kaiwa ko ina baki tunanin cewa nan gaba zata zo nemn danta?kuma asiri zai tonu? nace Allah zai rufa asiri, kai dai da safe mu sameta da batun muji yanda za'ayi.yace shikenan, Allah ya rufa asiri,to yanzu ina zata kwan?ka kaita dakinka,yace a'a, sai dai yara su dawo dakinki, ta kwanta acan , amma bazata kwanar min a daki ba, araina nace yanxun ba, amma da ai tare kuke kwana ma. yace kota kwana a falo? a'a ,bari in kaita dakin yaran.haka kuwa akayi,muka kaita can.Da safe dana kai mata abin kari sai tace a'a, tanada maltina da kuma biredinta, bata cin abincin kowane guri, da kanta takeyi, nace good, sannan na fita.mudai sama-sama mukayi bacci, kuma sama-sama muka karya, duk sai tunani muke, yaya kuwa sai nadama yake, dan dadin da yabi na watanni yaja masa zubewar mutunci na kila tsawon shekaru.misalin sha dayan rana yace in kirata ,muka zauna yara suna makaranta lokacin, ta fito sanye da riga da siket na jeans, kanta babu dankwali, cikinta kuwa har ya turo, ta zauna tana taunar cingam, yaya yace Mujidat dama mun kira kine don mu tattauna dake, shawara ta farko zanbaki dubu dari biyu ki zubar da cikin nan,ta daga masa hannu, ban amince ba ,koda zaka bani duniya da kayan cikinta, inbaka mantaba nafada maka, badan kudi nake tare da kai ba, sonka da kauna ce kawai, kuma cikinnan, (tasa hannunta ta shafa cikin)ribar soyayya ce, taya zan zubar dashi?kawo wata shawarar dai muji,kalamanta sun konan raina tamkar in tashi a gurin,amma sai na shanye.yace to naji, zaki zauna damu ki haihu, amma da sharadin baxaki fadawa kowa komai ba,duk abin dana fadawa mutane zaki tsaya akan haka ne?ta dan yi tsai tana tunani can tace ,zan yarda, amma idan na haihu meye makomata? zan tafi da danne?ko kuwa zan barshi anan?sai lokacin nasa baki , zaki

tafi ne kibar yaron a wurina, sai ki tafi abinki,wata ran,xaki iya xuwaki ganshi duk bayn wani lokaci, tayi min wani kallo, tare da yin kwai da cingam dinta kato, sannan ta fasa shi taci gaba da tauna duk muna kallonta, tayi yar dariya, in naki fa? cikin zafin rai Aliyu yace , sai ki tafi da cikinki, danma kin samu zan amsa? nasan uban dayayi miki? tace , ka manta dararen daka yi ta kwana dani?cikin bacin rai yace in baki yarda ba malam kizo ki fice min daga gida kije kiyi duk abunda zaki yi. tace zan fi son haka , dan zama gidan mamanka ze fimin wal-wala, dan haka zan je na fada mata ina dauke da jikanta, ta bani masauki, ni dashi muka kalli juna, yace kije man , zanfi san haka.nace , a'a ,kedai barshi a wancan tsarin,tace in dai har za'a barshi cikin sirri, tonima zan kawo nawa sharadin?Aliyu kam takaici ne ya hana shi daga kai, ban taba ganin shi cikin wannan yanayinba, na takaicida bakin ciki.nace fadi sharadinki muji?tace sharadina sai dai in na haihu zai AURE NI.... kalamanta na karshe suka tafi da numfashina, tsawon kiftawar ido, huhu, nayi nasarar janyo nimfashi na,idanuwana suka futo sukayi jajir, zufa ta ketomin, ta tuntsureda dariya har Aliyu ya dubeta, nima lokacin na dubeta, tace ,ya kika yi saurin firgita?naga keda mijin naki kamar tagwaye, shawarar ku daya, kun burge ni, kuma nasan yana sonki, kuma nima ina san shi dan nasan qualities dinshi, na baku zuwa gobe kuyi shawara.
(Uhm!Allah yakayuta,ANaM Dorayi)

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Aliyu ya harareta, Allah ya kiyaye ni Aliyu na aureki,ai ko zan yiwa matata kishiya na nemo mata yar mutunci bake ba karuwar titi,tir Allah ya tsareni, ya miqe, na baki awa daya kibar gidana, ko kuma yan sanda su zo su fita dake, da kyar na miqe kafafuna sunyi sanyi, dakina na

nufa don ko ganin gabana banayi,zuciyata tamkar ta faso ta fto,rigijif na fadakan gado, inasan yin kuka amma na kasa, lallai kuka ma rahama ne, tunda idan kayi shi zaka samu sauki, Hannuwanshi naji a gadon bayana, ji nake tamkar ya doramin wuta,zuwa,yanxu nasoma tsanar yaya Aliyu,gaskiya hakurina yana son ya kare, danzan iya danne komi, amma banda batun kishiya ,zan iya hakura ya aureta, amma kuma zan juri zama da ita?(Mata kenan,da kishiyar gida!..Allah ka karemu daga bin soye-soyen zukatanmu.....Ameen.ANaM Dorayi) Birkitonin da yayi shine ya katse min tunanina yace, haba My choice, kada wannan ya dameki, zanyi waya yanxun xa'a turo min yara su tafi da ita, xuwa ynxun ban damu duk duniya tasan cewa na mata ciki ba, ai nima dan Adam ne kamar kowa, ban wuce kuskure ba, nace aika riga ka tafka kuskure,dole ne ka aureta, kuka ya subucemun, naci gaba da magana cikin kuka wane hali Iya xata shiga in taji wannan labarin?ita da ba cikakkiyar lafiya ba, me zaka cewa y'ay'anka ? wadanda tun jiya suka damu dasan sanin wacece wannan bakuwar? y'an 'uwanka, wane idan kake dashi da zaka kallesu?su da sukeyimaka kallon mutunci da kima? ga abokai da sauran mutan gari?kada ka manta, shi fa mutunci madara ne, in ya zube sai dai a kwashi kasa,ka riga kayi abinnan da hausaw ke cewa TSALLE DAYA ME JEFA MUTUM RIJIYA....ya rike kanshi, sadiya na yarda duk wanda ya bar layin da aka ja masa a matsayinsa na musulmi dole yayi nadama mara amfani,danasan abubuwa zasu zama haka da banbi san zuciyata ba ,dam malamai suna gaya mana zuciya wata tsoka ce ajikin dan adam me hadari in kabi sonta sai ka halaka, ya dube ni, yanxu kin yarda? kinaga ba wata mafita sai ta auren ta? nace to inban yadda ba ya xanyi ,nasa masa kuka ina fadin na amince ka aureta, ,kallona ya dinga yi tamkar na zame masa wata sabuwa a sanyaye yace"nasan kin hakura ne saboda ni, amma nasan bakya san kishiya,amma kina ganin cewa nan gaba bazaki damu ba?na

runtse ido, zuciyata tana wata irin tafasa nace, batun zan damu ko bazan damu ba a ynzun ba shine mafita ba,na bude jajayen idanuwana ina kallonshi, sai dai ina fatan daga baya ba zka canzamin ba? ya rungume ni, Sadiya kada kiyi tinanin haka kada kiyi fatan haka, ki tayani addu'a Allah ya bani ikon yi miki irin halaccin dakikayi mini,banda kamar ki har abada,kuma ke kadai nake so ke daya kwal. Haka ya yi ta fada mini maganganu masu dadi da kwantar da rai, har zuciyata ta dan sauka. Yaya ya fito ya fita,ni kuma na kira Anty Abida na fada mata, ta ce hakan ya yi in ta haihu ya aure tan zai fi sauki a bakacin ta haihu ta ba ku yaron. Na ce, To ya zan yi tunda shi ya janyo. Nan dai muka yi sallama nafito na kuma dora abinci,sai dai ina gamawa ita ma ta soma dora nata,ban damu ba tunda neman sulhu muke. Misalin hudu yara suna Islamiyya suka shigo shi da Usman falo suka zauna, na kawo ruwa da abinci.Usman ne ya sha ruwan shi kam gogana har wata 'yar rama ya yi, ya kalle ni ya ce, Kira yarinyar nan. Na ce to. Na daga labulen dakin yara tare da yin sallama, ba ta amsa ba sai dai ta dago ta dube ni,rufdaciki ta kwanta kan katifar su Kausar tana chatting, na ce, Ki zo in ji Mijina. Ta yi min kallon kishi zan ce ko na tsana, sannan ta ja tsaki. Ni dai na juya na ce musu tana zuwa. Zan tafi Yaya ya ce in zauna, na samu guri na zauna. tafi minti shida sannan ta fito,munyi jugum-jugum kamar masu zaman makoki, ta tsaya kerere , gani. Ya harareta .Kizauna mana kin ce wani gaki? Ta zauna tare da fadin .yau kuma da wacce aka zo? Duk muka yi shiru, irin zaman nan da ake cewa mutuwa ta ratsa. Can Aliyu ya ce"Usman wannan ita ce Mujidat,kuma na maka bayanin komai,dan haka sai ka dan ce wani abu".Usman yace"bani da ta cewa,sai dai ke.ya nuna Mujidat,karkisake kice zakici zarafin wannan baiwar Allah ko nan gaba "yakalli Aliyu"ya kamata wannan ya xama cikin sharudan da zaka gindaya" Aliyu ya kalli Mujidat"na yarda in kin haihu zan aureki, amma ki sani so daya tak inayiwa matata ne,dole ki

bata girma da daraja,musamman data soma bazaman aure ba, sannan zaman haihuwarki ina gani can wani waje zan nemamiki haya" cikin sauri na ce ban yar da ba, ai ta zauna anan, kada a dinga zagayawa "Usman yace "haka ne kuma,amma kina ga batakura? Na ce "bakomai" Mujidat dadi ya rufeta ,kuma nan take ta nuna murnarta, ta kuma sake bayyana tsantsar san data ce tanawa mijina,dan haka dole tazauna dani, ban bari ta kai karsheba natashi nayi kicin abina.tsayawa nayi tsakiyar kicin shuru,anya kuwa ban yi wautaba?ban zalunci kaina ba?ban debo rvmuwan dafa kaina ba?amma sai wata zuciyar tace kedai kada kiyi wannan tnanin, tunda kin sadaukar da kimai ne dan asirin mjinki y rufu,Allah ya sani Zuciyarki daya da ita,kuma Allah zai shige miki gaba. Nasauke ajiyar xuciya nace Allah gani gareka,sai da suka fito ne naji muryar Usman na cewa"Madam na tafi"nace "ka gaida min su Ummulkhairh dasu walida"yace xasu ji.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

A ranar Aliyu ya koma Abuja,sabida an dameshi da kira,gida ya koma sai ni da ita saikuma yarana,a daren nan naje na fadawa Iya yanda muka tsara zancen,tayi ta tausaya mata,tare da shiwa yaya albarka tace ai gara daya taho da ita,tace in an barta sai ta koma ruwa, tabar musulinci, nace "ai shine" Iya tace Allah sarki, naxo in yi mata ta'axiyya,banda abinku, daba nan kuka kawota ba? Tunda ni kadai ce?nace"Iya ki barta can kawai,sabida bata jin Hausa sosai" tace"to shkenan ,kema Allah ya biya ki" na ce amin.

Daren ranar mun kusa rabashi a waya yaya yana shimin albarka tare da yi min alkawuruka kala-kala na riqe ni amana,tare da kyautatamin daji dani duk wani dadin zaman aure,har sai da aka

kira shi, yace minxai fta gurin aiki1 nce Allah ya tsare.
Haka muka zauna da Mujidat,bata min magana,sai dai ni in mata.innayi kamar in shareta,sai na tuna da haramcin gaba,dan haka in lokacin sallah yayi tana falo sai in ce mata"lokacin sallah yayi" wataran tace"to"wataran tayi min banxa ,sai dai ko ta amsa ba dole ne ta tashi tayi sallar ba.abinci kuwa,da kanta take yi,takanyiwa yara magana,amma ba wai wasaba, sai dai in tana san abu tace kai bani kaza, ko ke bni kaza. Sun dameni wai yaushe wannan bakuwar zata tafi? bata da kirki su suna san ta tafi,nce musu bazata tafib,Antyn su ce baban su ya kawota ,kuma tana da kirki,dan dai yanxun bata da lfy ne shiyasa.suka yi shiru badan sun fahimce ni ba,intaji fita tana san zaga gari sai dai kawai inga ta fice bako mayafi. Sai dai nayi masa waya nce ka fada mata in zata fita ta dinga saka hijabi ko mayafi, saboda an ce ta musulunta, in tana fta haka asiri zai tonu.ya ko kirata yace ta kiyayeshi.kar ta bari tayi abinda zai toxartata,tace ita bata da hijabi.yayi min waya wai in bata hijabai guda 2, sannan yace ya hanata fta,kuma ta sani ya zuba masu sa mata ido a unguwar, dan kar tai xaton cewa xata fita wani gantalinta ta dawo masa gida,ko kuma zata yo wani mugun abun.tace karya damu,dama ita burinta aurenshi, kuma tunda ta samu bata da matsala da wani namijin can waje, tana zuwa matsa jikine.
Duk wani zaman kunci na dauka a zaman Mujidat, sai dai ban damu sosai ba.ganin Aliyu baya sakar mata fuska sosai.komai tace masa tana so sai yace ta tambaye ni,bai cika zuwa gidan bama, sai daiyazo ya debemu da yara mu tafi can Abujan, akwai lokacin da sai da muka yi sati uku saboda yara sun samu hutu. Ranar da muka dawo har da shi ,mun samu ta tana kuka wiwi, wai bata da lafita,nce masa muje Asibiti, amota fadi yake Allah yasa ckinnan ya fta, na ce dan Allah kabari, ka mata addu'ar alkhairi, bayan dogon bincike likita ya gano tana shan maganin

tari na yara,wanda mata da maza kan sha sabida su yi maye. Likitan ya ja kunnanta da cewa in ta ci gaba d sha za ta kashe danta. Muna hanyar dawowa gidan na ce, Ki daina kada ki je ki yi sanadin rayuwar danki. Na dube shi. Kayi mata magana ta daina shan pakalin. Ya ce, 'Ina ruwana, ta yi ta sha indazata mutu ma kina ganin ba zan fi son haka ba? Ta ce, 'Eh, na san dama haka za ka ce, kuma sai na haihu lafiya. Na ce, 'Inma banda ke mene ne abin sha cikin maganin mura? Ya ce, 'Ai ba za ta daina rayuwar bariki ba. Ta yi shiru tana nazarin dalilinta na sha,tsabar son shi ne da take yi. Shi kuma ya kwashe Iyalan shi suka bar mata gidan shi yasa take sha sabida rage damuwarsa, ga shi ashe za ta janyo makanta ne, 'Yar shigarda ta samu a watse, don ta san in cikin nan ya zube shi kenan korarta zai yi batada sauran garkuwa za ta jure ta ci darajar dan da za ta haifa. Ta shiga wata bakwai lokacind ta cewa Yaya a waya wai tana son ta fara zuwa awon ciki, ya ce ta fadan in ta matsu.kin fada min ta yi sai shi ne ya tambaye ni. 'Mujidat ta yi miki batun awo? Na ce, 'A'a,ya fada min yanda suka yi na ce 'Ka bari sai ka zo sai mu yi zancen gani gata, in ya so sai a je Asibitin a kuma sayi duk wani abu d ake buqata. Bai amsa min ba ya canza zancen da cewa, 'Akwai wani bincike dazai kawo ni Kaduna me zan samu? Na ce, 'Duk abin da ka ke so. Ya ce, 'Yanzun ina takura sosai a gidana in na zo zan dauke ki mu fita a wani masaukin bakin mu dan' huta. Na ce, 'Yara fa? Ya ce, 'Ga gidan Iya. Na ce, 'To ma tafi mu bar mai ciki, kar a yi na wancan karon. 'A yi ta yi mana, ina ruwana, daman na san haka za ki ce. Ya ja tsaki tare d kashe wayar shi. Na sani tabbas rayuwarmu ta canza yanzun, amma wayaja? Shi ne. Allah yasa mu dace, ameen. Wata Asabar Aliyu ya nufo gida, yana karya kwanar unguwar su sai ya ga jama'a cirko cirko tsaitsaye gungu gungu, wadansu kuma suna ta maida yanda aka yi,yayin d kunnan shi ke dauko masa sautin wasu muryoyi suna ihun neman dauki. Kasancewar shi jami'in dan' sanda

dole ne ya bincika, don aikin shi ne kare rayukan al'umma da dukiyoyinsu, ko da ba a unguwarsu ya ga hakaba, dole ya tsaya.
Don haka ya gangara gefen titi yayi Parking din Motarsa,yana fitowane wasu matasa sin tsaya suna dan tattauna batun,Aliyu ya usa gurinsu fare da yi musu salllama,suka amsa,ya fambayesu abindake faruwa,daya matshin yagane Aliyu dan haka yace "yallabai wallahi 'yan sara sukane" Aliyi yace 'yan sara suka kuma? Yace eh! Wasu matasane ance daga hayi suke suka fada layinnan suma sara da sukan duk wansda suka ganiyanunamasa inda cincirindonbjama'a ke tsaye yace 'can meshayinnena Buba suka soka,sannan suka sari me lemun kysa dashi"
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Aliyu ya isa gurin daidai ana kokarin sashi amota yace "bakuyiwa yansada wayaba" ?wabi yace "tin dazu muka sanar dasu" Aliy yadagawaya yana sake miran yansanda yana shedamusu cewa a turomasa mota sabida 'yan sara suka sun sgigo ungywarshi ,shine yavasu damar kai masu jikin Asibiti sannan shikuna yacigaba da gudanar da bincike jafin isowar yansanda.
Tanbaya yaitayiwa mutaben gari kan yansara sukan;kasancewar mutanwnmu akwai tsoro da rashin cikakken wayewa ga wasu sai zuka mi bashi cikakaken hadinakai.sannanda yanufi motaesa dan karasa gida,sai yaji wasu matasa biyu suna magana,dayan yanacewa, "kasan Allah Aminu su Dawa Adone suka jamana wannan bala'indashi da Bangis Kauri" Aliyu yace "Kanina kananyfin Dawa Ado din tsokanarsu yayi?
Duk suja waiwayo suka kalli Aliyu,ganinshu da nayan Yansanda sai sukace a'a bamusaniba,suka juya da nufi.n tafiya Aliyu yace tsaya kuji absan cewa kunsan wani abu,dan Allah kubani

hadinkai.Dayan da akakira Aminu yace,'mufa zabcenmu daban, 'yansanda basu da amana,dazarar kafadi wata magana sai reshe yajuye da mujiya a kama mutum a tsare"
Aliyu yace ba gaskiya bane,shaci fadine da shrri irin na wasu mutane suke jifan jami'an tsaro dashj,mu masu kare rayukan Al'ummane da dukiyoyinsu bawai masu sharrib,kudinga bamu hadin kai,tahakane zamu iya gano bara gurbin al'umma."
Dayan wanda kebada labarin yace, yallabai yallabai tsorona kada a kirani shaida,suganeni insun fito suzo su sassareni".
Aliyu yace "sam sunanka bazai fitoba, vabu wanda yasan munyi haka dakai." Yadafashi. "Kagama zo nan mushiga daga mota dan kar wasu sugane kaine kafadamin,kayarda ba cutardakai zanyiba,taimako zanyi,kaga in ba'a dauki matakiba zasu iya dawowa.Zaka iya sanin ko kanwa tsautsayi zai fada?nasan kanada dangi,da mahaifanka, sannan ga kanka ko kanada yakinin cewa bazasu dira kankaba?
Saurayin yace "hakane yallabai"
Syka shiga Mota harda saurayin da dayan yace Aminu.
Aliyu ya kalleshi yace 'kanina kai ya sunanka? Nasandai abokinja shine naji ka kira da Aminu"
Yaron yace "Buhari'
Aliyu yace 'Buhari wane Dawa Ado?'
Buhari yace "Dan dabane,sunada yawa a ungywarnan,saidai su da bangid sune sukai kauri suna a ungywarnan"
Aminu yace, "wasuma sunce gudansu Dawa Ado ana siyar da wiwi,wasu yarsu dake zaman kanata agubta yake ajiyewa".
Aliyu yace "to mene labarin wannan fadan?"
Buhari gace,"to nidai mundawo Masallaci jiya da Magriba dayake layinmu daya da Dawa Ado,sai naganshi zaune tare da wasu yandaban,
,yaranema wadanda basufi shekara sha shida sha biyarba,yana fada musu cewa zamu fadawa 'yan hayi har naji ya anvaci sunan wani dan daban hayin yanacewa lallai yanaso ayimasa yankan da

bazai tashiba,ko yatashi kada ya moru.Nidai na wuce nabarsu,saidai ina zaton kan wiwi ne sjke fadan, dan naji yanacewa "ankawo mishi kaya kafin yazo shi wancan ya siye"
Aliyu ya girgiza kai alamun gamsuwa yace, to yanzu kuyimin kwantabcen gudansi Dawan dakuma Bangis din, ' sukace to.
Nan sukayimasa kwatance yacuro kati mai dauke da lanbarsa a jiki ya basu,.
"Gashi kusa lanbobina a cikin wayoyinku,sai ku kirani ko kumin flashing inkira dan insamu taku lanbara,kunsan dalili?
Sukace a'a. Yace dan kucigaba da bada gudun mowa cikin hnguwar nan,duk lokacin da kukaga wabi abu mo kukaji makamancin wannan sai kuyi maza kukira daya daga cikin wadannana lanbobin. Ya sanya hannu ta baya yaciru yan dubu dubu guda biyu ya mika musu tare da cewa,"Ba cin ganci vane kyauta nabaku,aikinmuma dazakuyimin ba na kudibane taimakon kaidakai zakuyi."
Da murna suka karba, sunyj masa godiya,take nan suka bashi lanbobinsu,sannan suka gangara inda suja nunamasa gidansu Dawa Ado da Bangus Kauri.sanna ya gan ga ra ya ajiyesu ya wuce hidansa.
Likacin d na ji kwankwasa kofar ina kicin ina kokarin dafawa yara Indomie, don ni a koshe nake Iya ta aiko min da dambu, nacishi sosai bayn La'asar shi yasa. Na nufi kofar cikin raina ina tunanin ko waye? Ina bude kofa na yi sororo don bai fada min zai zo ba. Na ce, 'Oho! Abin 'Yar haka ne? Ya shigo, sannan ya rufe kofa, ya kamo ni ya rungume, na karbi jakarsa muka nufi ciki. Mujidat tana zaune a falo ta ce, Sannu. Ya ce, 'Yauwa. 'Ba tare d ya kalletaba. Muka nufi dakinsa ina fadin. Kausar, Al'amin ga fa babanku. Da gudu suka fito dga dakina, muka dunguma dakinsa mu duka. Na ce daka fada min kana zuwa Allah d tuni na yi maka abnci na musamman. Ya ce, 'Ai rikici na tarar a unguwar shi yasa da tuni na iso. Na ce, 'To yanzun me za ka ci? Ya ce, Me ki ka dafa? Na ce, Ban dafa kmai

ba, yanzu daizan yi wa yara indomie,sai dai muna da miya a fridge sai na dafa maka farar shinkafa. Ya ce, 'A'a ku tashi muje gidan cin abinci. Na ce, 'To ka canza kaya mana, ko kuma ka yi wanka. Ya ce, 'Duk yanda ki ka ce. Na dubi Kausar 'Mu je in ciro muku kaya ki sa musu sai ke ma ki sa.'Na dube shi. 'Bari in ba su kaya. Gira ya daga min na fita. Na dawo na taimaka masa ya yi wanka. Ya shirya, nima na canza kaya, duk Mujidat tana zaune a falo tana kallonmu, sai na ji tausayinta ya tsirga a raina, na ce, 'Ki tashi muje cin abinci. Saida ta yi min wani kallo, sannan ta ce, 'To. Mun fito sai ya Aliyu ya ganta, ya ce, 'Ke fa? Da sauri na ce, 'Tare za mu je mana. Tsaki ya ja,sannan ya ce, 'Ni yanzun ba nida damar sakewa kenan? Ban tanka masa ba, a raina na ce wa yaja? Lokacin dakuke shanawar ku ai ba ka ce an hana ka sakewa ba. Da farko yaso mu ci a can,amma yanzun sai ya ce kawai mu yi take away sabida bai so zuwanmubada Mujidat. Daga nan sai ya nausa da mu can gurin kasuwar Bacci, wani katon shagon saida kayan wuta, na ce me za mu yi anan? Bai kula ni ba don na lura ya ji zafin zuwan Mujidat. T.V ya sai mana ta bango (Plasma),mai kyau sai tsada,sannan ya sayi resiba,ban san inda zai sa ba. Sannan muka je wani babban store ya kwasarwa yara kaya har da keke ya saiwa Al'amin. Yara sunata murna muka isa gida. Ita dai mujidat duk inda muka je da Ido take binmu, tare da yatsina fuska,jifa jifa tana tabe baki tare da tsaki. Ni dai muka yi ciki ta zauna a falo.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Dakina ya kai T.V, na ce ba na ka ba ne? Ya ce, 'A'a naku ne,don na lura ke da gidanki,amma kin bar wa wata falon ki. Na tsura masa ido, 'Yaya na gode. Ya harare ni, Lokacin fa dakika samin

suna kin yi alkawarin kirana Sweety Alinki,amma yanzu sam kin daina na manta rabon da ki kira ni dawannan sunan. Na ce, Yi hakuri Sweet dina. Sai na ji su Kausar da Al'amin sun sa dariya.Kausar ta ce, Momy Abba ne Sweet? Muka kalli juna cikin dariya na ce, 'O.K, waton kun tsaya jin mu ne? Al'amin ya katse zancen da cewa, Abba wai ita Anty bakuwa sai yaushe za ta tafi? Kausar ta zabga masa harara, 'Ina ruwanmuda wata can Anty Bakuwa. Muka sake kallon juna cikin mamaki. Na lura fa Kausar ta tsani matar nan. Nace, Kausar ai ba tafiya za ta yi ba ita ma ta zama 'yar nan gidan. Kausar ta zaro ido, 'Ta zama 'yar gidan mu kumma? Ta tura baki,ni dai Abba ta koma gidansu, kullum sai ta dinga hararata, ko kuma tayi ta hana mu kallon T.V. Na ce to ba ga shi Abbanku ya siyo mana wata ba? Ta yi shiru. Na ce, 'Kar ki sake yin haka. Ranta a hade ta ce, to Momy. Mun ci mun sha muna ta hira har yara suka yi bacci, sannan muka gyara masu kwanciya, sannan muka nufi dakinshi.Yayo alwala tare d cewa. Je ki yo alwala muyi Isha'i. Na yi murmushi , sannan na ce, Wanka zan yi don ina fashin sallah. Ya runtse ido tare d fadin, kash! Ga shi gobe zan tafi. Na ce, Kar ka damu zan yi maka irindabarun da muka sabayi da. Dariya ya yi, sannan ya ce, shi kenan. Da safe ni mkadai ce na fito na hada abin kari, sannan yara suka ci suka fito. Babansu yana kwance na ce 'Bari in kai su makaranta. Ya mike. 'Yau ba Lahadi ba? Na ce, 'Hadda suke zuwa Asabar da Lahadi. Ya ce, 'To ki yi sauri ki zo ki kara yin wata dabarar. Na yi masa hararar wasa. 'Bashi yasa na ce amAuran Mujidat zai taimaka maka ba ya hade rai, sannan ya koma ya kwanta. Na dauki makullin motarsa. Bari in ari motar ka. 'Nan ma bai tanka ba. Lokacin da muka tafi Mujidat tana soya kwai a kicin, na cewa Kausar su je su gaida ta. Kullum dama sai na sa su sun gaishe ta, kamar kullum sai d ta yatsina fuska sannan ta ce, Lafiya. 'Na fita abina. Mujidat tana ganin fitar Sadiya da yara sai ta maida kofar ta rufe,sannan ta nufi dakin Aliyu yana kwance sai ya ga mata

tsaye a kanshi tana girgiza. Zumbur ya mike tare d fito falo, don gudun kar ta kara janyo masa wani laifin a kan na da. Ita ma ta biyo shi tana yi masa kallon banza kana tsoro kada matar ka ta dawo,shiyasa ka fito kar ta same mu tare.ta yi 'yar dariya. 'Ai ka gama kuskure tunda har kayi ajiya a jikina na zo in yi maka gargadi ka rage nuna tsana da kyama gare ni, in ba haka ba na rantse maka zan je gidan mahaifiyarka in tona komai. Aliyu ya ce,'Ai har abada ba zan so ki ba, kin ci darajar matata data dage sai kin zauna da mu, banda haka ke din banza. Ta tuntsire da dariya, 'Ai ba ka san wani abu ba, ai ita kan ta matar taka sa'a ta ci d ta kasance mai son kwatanta adalci, banda haka wallahi da sai ta raina kanta a wannan zaman da nake yi a gidan nan, don sai dai inmu dinga kwana da kai gado daya.ya harare ta, Ni kuma da yake zan tsaya ne ina kallon ki har ki shigo mini daki,kuma ki sani ni Allah ya shirye ni. Ta ce, 'Oho! Yanzun kana tsammanin cewa kai wani shegen mai imani ne? Ta yi murmushi mai sauti,sannan ta girgiza kai. 'Abu daya zan fada maka shi ne ka gode min da na kawo shawarar auren ka,sannan ka godewa matarka da ta yarda da in aure ka,ta samawa kan ta lafiya don wallahi da sai dai ta sallamawa kan ta domin matsawar ina numfashi duk inda ka ke sai na bi ka,kuma sai ka yi duk yanda naso. Ya gyara zaman shi sannan ya ce, 'Kin yi kadan shaidaniya. Sannan ya kautar da kai.sam bai tsammaci zuwan ta ba,sai dai ya ji ta a jikin shi 'yar barikin ta san lagon shi,wanda baya iya bijiremata, zuciya muguwar nama har za ta amince,amma sai Aliyu ya yi ta maza ya hankade ta duk d tana da ciki, sannan ya ajemata mari a fuska,ta shafa kumattun tana kallon shi bayan ya mike yana mata kallon banza,ta yi 'yar dariya. 'Dubi yanda idanunka suka canza launi, ban da cikin jikina da sai na tabbatar maka cewa in ina nan dole ka rayu da ni,Kasa ba ta amsa ya yi kai tsaye ya nufi dakinsa ya shiga ya kullo kofa,sannan ya zauna bakin gado tare da rike kan shi ya ma rasa wane irin tunani zai yi.Can

kasan makogwaron shi 'Hasbunallahu Wani'imal Wakil yake fadi can a hankali ya ji kmai yana warewa, ya kwanta rigingine ya tabbatar cewa Mujidat shaidaniya ce, za kuma ta yi duk abin data fada, auranta kam shine mafita, inbahaka ba zata jashi zuwa wuta,tunda in tana raye bazai fasa zinaba.Yadauko wayar shi ya soma kiran layin matar shi.

Ina daf da gida naji wayata tasoma ruri, nayi kwana,sannan na daga. 'Yaya dai Sweety Aly? Ya ce, 'Ina kikene? Kin san dai daga ni sai wannan shaidaniyar a gida. Gabana ya fadi, sam ban tuna haka ba,nace 'ga ni nan yaya ina daf da gida. Ita ce ta bude min gida lokacin da na buga,sai dai tana bude min ta juya a raina na ce, 'Hakan ma nagode. Na aje mota,sannan na nufi ciki. Zaune na same ta tana sanye da dogon wando na jeans, sai 'yar best yanayin shigarta na bata min rai, musamman in yaya yana gari. Na murda kofar na ji ta a kulle, na kwankwasa ya bude na bi shi da kallo, don son in fahimci wani abu, amma ban gane ba, don haka nace. 'Lafiya? Ya dube ni, 'Me ki ka gani? na ce, 'a'a bakomai.naga kakirane na dadene? Ya ce, 'a'a, kin san ina jiranki ne a sake yi min irin dabarar jiya.nayi dariya, 'ai bana batun dabara barima inyi wanka don ina zaton anjima zan yi sallah. Damurna yace, 'Haba? Na ce, 'Allah. Ya ce to shiga ina jiran ki. Saidai kuma ina fitowa na same shi zanzare cikin kakinsa yana daure takalmi, sororo na tsaya cikin mamaki kafin nayi magana sai wayarsa ta soma ruri,ya dauka da sauri. 'Buhari inajinka. Daga inda nake na jiyo wanda ya kira da Buhari yana cewa,Yallabai muna zaune ya wuce kamar yanda nasoma fadamaka dazun, shi Dawo Ado, malun malun yasa yana riqe da Adda sannan malun malun din ta jike sharkaf da jini. Aliyu ya ce, 'Dan uwanka Aminu ya kira ni ya fada min wai 'yan sara sukan nan sun ce za su sake shigowa anjima, zan fito yanzu. Yana 'aje wayar ya dauki dayar ya kira headquater ya buqaci a turo masa 'yan sanda mota biyu. Ina mamakin yanda Yaya keda izza cikin aikinsa, yanzun nan ya rikide daga soyayya

ya kma zakin maza,ya kama kofa zai bude nace "Sweet aliy ka manta daniko?" ya waiwayo da sauri, sannan ya dawo ya rungumeni jikinsa ya sumbaci kumatuna"ya za'ayi na manta dake? Ashe zan iya mantawa da kaina kenan?ya dago fuskata"sai na dawo"na saki murmushi"Allah ya tsare min kai mai sona"ya sakeni ya fta da sauri.
Sun kama Dawa Ado,Bangis Kauri, sannan suka dinga fadin sunan yan daban suna kama su.kazalika sun dire hayi,inda can ma suka kamasu da yawa,ya mikasu yakuma basu shawara cewa suyi bincike kan yaran sosai.sannan su tabbata sun mikasu kotu.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Hakanan da dare ina Sallah a dakina,misalin takwas wanda yanzun yazama na yara,Kausar da Al'ameen suna kwance ruf da ciki suna Homework ,Aliyu ya shigo da Sallama,suka amsa tare dayi masa sannu da zuwa,ya kalli Mama dake bacci can gefe yace"wai shin mamana tayi nata Homework din ne? Kausar tace"eh Abba sunyi tare da mumy"dai-dai lokacin na kammala addu'a ya tayani shafawa, na kalleshi"sannu da zuwa" cikin murmushi nayi maganar yace"yawwa,sannu matata"muka sa dariya, ya rusuna saitin kunnena yace "kisa yarannan suyi bacci da wuri" kafin in bshi amsa wayar shi tasoma ruri.ya daga da sauri,nji yana fadin "Yes Sir" nace Allah yasa ma zaiyi kwanan gdan yau. Ilai kuwa, yana gama wayar ya kalleni" yanzunnan zanwuce Abuja" na zaro ido"Abuja kuma da daren nan?" yayi dan yake"aikinmu kenan, ahaka muka yi rantsuwa babu dare ko rana,duk lokacin da aikin yataso zamu fuskance shi"na lumshe Ido ahankali nace"yanayin aikinku yana shafar rayuwarku"ya mike zumbur"muje ki hada min kayana" Kausar ta tashi zaune"Abba bari muxo mu rakaka motarka"nace "a'a , ci gaba

da Homework dinki in yashirya zaizo har nan sai ku raka shi," tace to. Tara dai-dai ya kammala komai,dan ban amince ya tafi bai samu nutsuwa ba, sabida tsoron kada shaidan ya sake ribatarsa ya kuma kyallo wata,lokacin da muka zo gurin su Kausar tini duk sunyi bacci. Ya tsuguna duk ya sumbaci kumatunsu, sannan ya dauki hanya,na raka shi mota,sai daya tashi sannan na koma ,ban tsaya wani tunani ba na kwanta don Inda sabo na saba da tafiyar Yaya cikin dare, sai dai Adduar Allah ya kare min shi.
Kusan sha biyun daramen wata litinin na jiyo ihu cikin baccina, na tashi da sauri ashe nakuda ce takama Mujidat. Da gudu na fada cikin dakin tana zaune dirshan tana juyi da ihu, na ce ta kwanta, bari na gani ko mota ta da mai. Kafin na dawo har kan da ya fito sai ihu take har su Kausar sun tashi nace mota ta ba mai bari in kira Iya. Na kira ta na fada mata, tacebari ta taho tind dare bai yi Sosai ba. Kai Mujidat akwai raki, har nadaina Jin tausayinta, sai dai haushi.Kafin Iya ta shigo dan ma Ya fito, masha Allah jariri sambalele, sai dai abin ya yi ta fadar da gaba na yadda naga yaron tamkar Yaya. Iya ce ta yanke cibi sannan muka gyara ta tsaf da danta. Kusan 3 dare suka samu bacci, Ni da Iya muka koma dakina. Ta dubeni. "Sadiya!" na kaleta da faduwar gaba. Tace, "jaririn nan baki fahimci komai ba?" Na girgiza kai "A'a iya ban fahimta ba. Bashi da Lfy ne?" Tace, a'a kama naga yana yi da mijinki sak, tamkar an tsaga kara, ko 'ya'yanki basu yi kama da shi ba kamar wannan yaron, tsorona daya Kar dai ace Gadanga ciki yayowa wannan yarinyar. "Nayi saurin cewa, "a'uzu billahi! Iya ba kyau ayiwa mutum mummunan zato, kin San wannan ba halin Yaya bane". Ta ce 'eh, to haka ne, amman fa mutum yakan canja daga halinshi da aka San shi dashi." na ce, a'a fa iya ita fa wannan da mijinta, kafin ya mutu mun sha gaisawa da shi. Kuma shi kamanni hakayake sai kiga baku hada komai ba amman Kuna kama." ba don Iya ta gamsu ba tace to Allah yasa hakanne. Na ce ameen. Nan

mukayi alwala muka kama nafila, addua ta Allah
ya rufawa mijina asiri Kar duniya ta gane wannan
matsalar.
Da safe lokacin da na shiga dakin tana zaune da
danta a hannunta ta tsura masa ido tamkar ba
ita bace tayi ta kurma ihu ba. Na ce 'kin tashi?"
ta ce, 'eh mun tashi, kin ga yarona sai kace
Babanshi, naji dadin haka,Dan bazai sake min
musu cewa ba cikinsa bane." da sauri na ce,
'kibar maganar nan mana, yanzu bari kuyi wanka
in na kai yara makaranta sai nazo na kai ku
Asibiti." ta yatsine baki "kin sanar da mjnki?"
nace, a'a kin San Iya tana nan ba dama in masa
zancen ki.' ta dauko wayarta tana cewa, "ina
ruwana da Mamansa taji. Layinsama a kashe
yake.' tayi tsaki ta jefar da Wayar, Ni dai na fice
na kama aiki na raina bace, ban cika ganin
laifinta ba Dan shine musabbabin komai.
Da zamu Asibiti na sauke Iya a gida na wuce
dasu. An duba su ance duk suna lfy, muka tsaya
kasuwa na siya abubuwan da basu da shi,sannan
muka nufo gida.
Tsakiyar gado na zauna sannan na soma Kiran
layin mijina, bugu biyu ya daga, nayi Sallama ya
amsa tare da cewa. "Yaya na jiki cool da yawa?"
Na ce, 'Yaya budurwarka ta haihu." budurwata
kuma? Ya fada cikin sauri. Na ce, eh Mujidat
danta yana nan namiji......zandakata a anan zuwa
wani lokacin kuma,fatan zaku kara hakuri dani
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai
masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Zaharaddeen Shomar
Whatsapp 08168575100

Darajar Yayana2-03
Posted by ANaM Dorayi on 04:31 PM, 23-Mar-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
_________________NA
___________HALIMA K/MASHI
Ta soma kwalla a kwai su, amma sun zo sun kasa kamo barawon.Ya ce, to daga sun zo ne zasu kamo barawo kamar suna da Allahn musuru?Ina ganin ki hakura kawai in ba a kwai wanda kike zargi ba.Ta ce, cikin jaka ta yake a dakin na, ni na tafigidan kawata, mama ta tana shigowa sai kanena sun ce kuma basu ga wanda ya shigo cikin dakin ba.Aliyu ya tabe baki.Shirme kenan, sai ki hakura kawai.Ta mike tana share hawaye, shi ke nan nagode.Sanan ta tafi.,har ya gama shirin sa tsaf zai tafi sai ga wayar commissioner yana neman sa yana isa aka dan ka wani aiki a hannunsa.Dole ya fasa tafiya ba don ranshi ya so ba.Washe gari ranar goma dai dai dawowar shi ke nan daga wurin motsa jikin da yaso xuwajiya hakan bata samu ba sai yau. Waya ta buga daga bakin gate ne, mai gadi ya ce, yallabai bukur jiya ce ta dawo.Cikin damuwa take oga.Dan sanda ya kara da haka ne don don tunanin cewa in ta fito yau ma zai sami kwaleliyar dubu daya tamkar jiya.Aliyu ya ce ka ce mata zan fita ne ta dawo da yamma, bata jin dadin haka ba amma me nema yana tare da samu, don haka sai ta hakura ta tafi.A ranar ta saka hotonta da ainihin sunanta aaccount din da ta bude kuma Aliyu ya amshia botar ta.Da yammancin ranar bata zo ba domin ta dana sabon shairi, sha biyu zuwa karfe dayan dare ta san lokacin da take ganin shi a online ne, don haka sai ta hau.Cikin sa'a yana nan ta soma da tura masa hotonta a inbox, yana ganin hoton ya gane ta.Ya ce, oh, daman ke ce kika yi mun basaja don in karbeki?Ta ce, naga in ba haka nayi ba ba za ka kulani ba.Kuma ina da matsala kai ne nake ganin zaka magance mun.Aliyu ya ce matsalar me?Ta ce, kafin in fada maka matsalar tawa, ka fara kallon hotunan nan.Aliyu ya ce, to.Duk a tunanin sa matsalar ta ta shafi

aikin sa ne.Matsalar farko sassan kirjinta ne, haka ta turo gabobi duk tsiraicinta ba inda ta babu inda ta rage.Ya ce me nene ma'anar hakan?Ta ce, ka duba hotunan da kyau?Ya ce, eh.Dama ina so ne ka gani da kyau don in nayi maka saimatsalar tazo da sauki, domin tun ranar da na ganka na haukace da sonka.Ka taimake ni.Aliyu ya rasa me zaice don ta kaici da bakin ciki, sai kawai yayi blocking din ta amma mehotunan da ta turo sun hau cikin hotunanshi.Ya dinga bin su da dai dai yana sharewa, amma da yazo kan na farkon na kirinta sai ya tsaya yana ci gaba da kallon hoton har ma ya kasa goge shi.Cikin daren tunaninsa ya soma gurbacewa, da safe karfe shida wayar bakin gate ta shigo, bai dauka ba don lokacin bacci yana kanshi.Don baiyi wani bacci ba can kuma a bakin gate din shi kanshi mai gadin yana son wanan bakuwar ta samu shiga sabo da ya san in ta fito zai samu wani abu.Ya ce, madan me yasa jiya da yace ki dawo baki dawo ba?Ta lallaba jakarta ta ciro yan dubu guda biyu, gashi kasa kati.Da sauri ya amsa ya tura a aljihu kamar yana tsoron kada wani ya amshe masa, ko kuma ita ta ce ta fasa.Ya shiga zuba mata godiya, ta ce, tunda jiyaya ce na dawo ban dawo ba me zai hana in shiga kawa yanzu?Dan sandan ya zaro ido oga yana da ka'da sai dai in yayi fada zaki fiar da ni?Tayi masa fari da idanunta, kada ka damu inyayi fadan zan wanke ka.Tun da shiga falon ta ke ta kalle kalle, falon nashi ya birgeta duk da cewa ba wani kayanalatu ya zuba ba.Ta zauna kan kujera ta bude jakarta ta dauko hoda da turare ta sake gyarawa.Sanan ta cire rigar sanyin dake jikinta saura singilrti, ta ajiye mayafinta ta gyara gashin dokin dake kanta.Sanan ta dauki wayarta ta soma kiran wayar ne ya tasheshi, wata isaka yaji tana kadawa tamkar za ayi ruwa.Windo ya nufa ya daga labule kamar yanda ya zata, hadari ne, yaji dadin haka ko don yakara mikewa.Wayar ta sake kacamewa da ruri, yana dubawa yaga number yarinyar, tsaki ya ja tare da yin jifa da

wayar kan katifar sa.Ya bude kofar nifinsa yaje kicin ya samu abin tabawa, cak ya tsaya sabo da ganin yarinyar gaban shi ya soma faduwa, lokacin da zuciyar shi ke tuno mashi hoton.Yayi karfin halin daure fuska, sanan ya ce, da izinin wa kika shigo min gida?Ta mike ta nufosahi, da izininka masoyi na, ka manta ka ce in dawo jiya? Ban sami dama ba shine na dawo yau.Ya ce, to fita a gidan nan fita, ya nuna mata hanyar waje.Ta zauna a hannun kujerar dake kusa da ita,da ma ka bari mun fahinci juna.Ya juya ya shiga dakinsa a fusace, durowa yaje ya dauko bindiga nufinsa yayi mata barazana.Ya fito da ita ya saita ta, kwashi kayanki ki fita.Hakika gabanta ya fadi don bindiga ko makerinta yana shakarta.Amma duk da haka sai ta jajirce, ta runtse ido hawaye suka soma zuba,zanfi so ka kasheni feye da ka barni a raye amma baka amshi soyayyata ba.Zanyi alfahari in ka kashe ni da kanka, kuma kacewa jami'an tsaro ni na yafe maka ko sun tsinci gawata a gidanka.Aliyu ya ce, muje ki fita ni bana son jin komai daga bakinki.Sun isa bakin falo Ruwa ya tsuge mai karfi wanda hakan ya sa ya kyale ta.Ya shiga daki ya adana bindigar, sanan ya hau katifar sa ya kwanta.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Gurbataciyar zuciyar sa ta shiga kitsa masa wasu abubuwa, dauko wayar sa yayi yana kallon hoton da yarinyar ta turo masa.Cikin jikinsa sanyi yake ratsawa na ruwan dake sauka.Mujidat turo kofar dakin ta shigo, kasa magana yayi lokacin da ya waiwayo yaga ta raba jikinta da tufafi.Yayi ta maza ya daka mata tsawa, mai makon ta fita sai ta nufo gurinsa da gudu ta fada masa.Shedaniyar shu'uma ce yarinyar, don haka bata samu matsala sosai ba

gurin amincewa da gayyatar da tayi masa, zuwa ga fadawa tafkin zunubin shedan ya sake kawata abin ga zuciyar Aliyu.
Har yake ganin haram ta shigeshi fiye da halalinsa.Mujidat ta amince Aliyu ne irin mijin da take so ta samu.Duk runtsi ba zata barshi ba, sai da kanwa takar tsami kwannafi ya kwanta.Aliyu ya shiga jin cewa bai kyau ta ba.Na dama ta shigeshi, ya mike cikin bakin rai ya nufi ban daki zuciyar shi yar bakin ciki tana tunanin shi cewa, wanan wankan da zaiyi anya zai fidda mai da dattin zunubin daya kwasa?Ya fito ya same ta kwance, haushinta ya kamashi sosai.Ya dauki makulli ya bude durowarshi ya ciro kudi batare da ya irga ba yan dubu dubu sabbi ya mika mata.Gashi an gama ruwa ki tashi ki tafi na rokekikar ki sake dawowa gidan nan.Ta kalleshi cikin damuwa an ce maka neman kudi nake yi?Ta mike ta soma saka tufafinta, so da kauna kurun nake nema a gurinka baka da kudin da zaka iya bani.Ta fice ta dauki jakarta yana tsaye a tsakiyar falo yana kallonta ta fita tare da cewa sai ka sake jina.
Ranar Aliyu yajima bai fita ba, na shi ganin mutane zasu gane abin da ya aikata, kuma sam baya son ya tuna.Sai istigifari yake yi, in dai haka mazinata suke ji lallai zina bala'ice, ya gargadi masu gadinsa lallai kada su sake barinta ta shiganmasa gida.
Mahaifiyar mujidat yar asalin wani kauye ne a Ilorin can jahar kwara, an ce dai asalinsu fulani ne, amma yarbanci suke yi kuma yarbawa suke kiran kansu.Musulmine su amma musulincin nasu sai a hankali.
Mahaifiyar Mujidat mai suna Bukolatayi aure da Mahaifin Mujidad hakimu bayansun haifi yayan Mujidat dan suna fari kenan, mai suna Latif.Wanan al'adar yarbawa ce mace taje aure amma sai ta haihu za a daura, tasu hikimar wai a gani in mai haihuwa ce.Bayan Latifa sun sami Sikirat sanan Mujidat, mahaifin su mujidat direban taxi ne, mahaifiyar su kuma tana da shago a bakin kasuwa.Tun tasowar Mujidat bata

ji sam yar karya ce da son bobo, tunda ta lura tana da kyau ai sai ta mai da kyawun nata tamkar abin kasuwanci. Tun tana shekara tara ta soma amsar kudi tana fansar da mutuncin ta, haka ita mahaifiyart fitina gareta ko yau she tana biye da mata wanan ya sa ko karatun kirki bata yi ba, tana secondary idanunta sun gama budewa, manyan mutane suke daukanta.Da farko iyayanta sunda mu don mahaifiyarta ta sha yi mata duka sanan tayimata tsarki da ruwan barkono, amma da ga baya da ta soma harka da manyan mutane tana kawo musu kudi sai suka shiga shi mata albarka.Haka nan basu damu tayi wata bata zo ba in dai zata yi musu aike.A zuciyar su tafi yan uwanta Latifa da Sikira wadda take aure a garin Ilorin.Kuma dalilin ziyarar da ta kawowa anty sikira ta hadu da Aliyu.Kuma har ta koma gida so da kaunar Aliyu yasa ta ta dawo Ilorin don samun muradin ta.Jin kai da jan aji irin na Aliyu shi ne ya sake burge ta, amma sai gashi tashin farko ta same shi cikin sauki.Tabbas in ta nace ba da dadewa ba zai zo hannunta.Karfe tara na dare ta kira numbar wayan mai gadin gidan Aliyu wanda ta amsa dan bukatar kanta.Bayan ya daga ta tambaye shi ka ganeni?Ya ce, a a ban gane ki ba.Ta ce, sanana Mujidat daga nan cikin gari ni ce wace na amshi numbar ka jiya bayan na fito gurin Oga ya ce, ok madam ce ko?Sorry madam na gane ki, ta ce oganka ya shigo?Ya ce, eh, tun bakwai yana gida kuma naga alamar ba zai fito ba, sai dai yayi mun kashedin cewa ko kinzo kada in barki.Mujidat tayi shiru tana mamaki, me zai sa ya tsaneta haka?Duk da ta mika masa kanta kyauta, amma sai tayi wani murmushi.Indai kissa tana magani to zatayi mun, ta ceda me gadi in na baka dubu biyar yaya zan samu in shiga?Yayi shiru yana nazari.Lallai yana bukatar kudi don yasha kan matsalarshi da maman Bilikis, amma dubu biyar yayi masa kadan.Yace madan zan iya dabara in kin ban dubu goma, zan fadawa Oga cewa mamana ba lafiya nasan zai barni in tafi.Don

haka ta ba faruwa amma nasan kafin inbar wurin sai an kawo wasu lokacin ke zaki samu shiga dan su basu sanki ba.Kuma kafin in tafi zan lalata wayar cikin gidan, ta ce hakan yayi zan sameka da kudin in ka kamla komai ka kirani.Yana kashe wayar yaga Aliyu tsaye a bayan shi
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Dfarko ya rude sai kuma ya tuna cewa duk sun yi maganar ne cikin yarensu na yaroba.Aliyu ya ce, ina ta kiran waya baka daga ba?Ya ce, oga jikin mama ne ya tashi shine dan uwa na ya kirani.Aliyu ya ce, jikin ta ya sake tashi?Wani ciwo ne ke damun ta?Ya ce hawan jini ne, Aliyu ya sa hannu ya lalubo dubu biyu ya mika mashi tare da cewa, Allah ya kara sauki. Ya kara da cewa kaje ba sai ka jira wasu ba, bari nayi waya su zo.Da murna mai gadi ya fita ya kira mujidat yace, tayi sauri kafin wasu masu gadin su zo.Cikin sa;a ta tura kofa ta shiga, haka nan cikin sa'a ta riske shi a cikin falo zaune da yar shirt fara irin mai kama jikin nan.Sai gajeren wando, kalkon labarun kasa yake yi NTA, turo kofar ne yasa shi waiwayawa, zunbur ya mike yana nuna mata waje.Fita la'ananiya, ta saki jakarta ta nufeshi, haba masoyina, ina sonka sosai tsaya kaji.Ta kai hannu zata taba shi ya ja baya.Ki fita kawai, ta zauna kan kujera, ba zan sake barin gidan nan ba ko zaka kashe ni.Ya biyota ta zagaya ta fada bedroom dinsa.Ya rasa me zai yi mata, sai kurum ya kira yaransu daga headquarter, jin haka dama tariga ta tanaji dabbararta.Taciro wayarta ta danna wani hoto ita da shine suna tsaka da aikata masha'a ta dauko.Kalli hoton nan ka gani, ina da irinsu da yawa har na kati na wanke.Aliyu ya fizgi wayar ya kalla, duk da ya girgiza amma bai nuna mata

ba ya ce, yace amshi wayarki ba kati ba in kin gadama in kin tashi ki sa shi a kan profile din ki na fcbk,ko a jikina.Ke ce mace mutuncinki sai yafi nawa zubewa.Tayi shiru ta rasa me zata ce, ya ce fita.Ta daga hannuwa biyu, naji naji zan fita, ta matso gunsa amma ya kamata a ce kanayiwa mesonka kallon mutunci da kima.Ta soma kuka, ka tuna ba nice na dorawa kaina sonka ba, ya kamata ko baka sona saika fada min magana mai sanyi.Ya runtsa idanu, burinsa ta fita domin zuciyarshi ta soma tausayinta.Sanan ga shi dan can gefe yana rada masa wani abu.Ya bude ida nunshi, shi ke nan naji ban kyauta ba amma dai yanzu ki fita kawai, domin ni da ke ba hurumai bane.Ki tuna da abin da ya faru ni dake she karanjiya laifi ne babba, kin sani.Ta matso ta kama hannuwansa ka min afuwa sonka ne ya sani haka.Yanzu ina jin yunwa ko zaka tai maka min da wani abu in ci sai in tafi?Ya ce, duba kicin sai dai in bread za ki ci.A kicin tayi ta zagayawa tana tunanin me zatayi ne don ta samu ta kwana a gidan.Ta dauki wuka ta dauko bread wai za ta yanka, amma sai ta kulle ido ta sharbi yatsanta da gangan, sanan ta saki kara.Cikin hanzari ya nufi kicin da ganin yanda jinike zuba ya sa shi shiga da sauri ya rike ya tsan nata.Kasancewar yana da yar akwatinshi ta taimakon sai ya gyara mata ya rufe shi sanan ya ce, muje a maki Allura sai ki wuce inda kike.Ta soma rawan sanyi wai ba zata iya tashi ba, barinta da yayi ta dan warware shi ne ya kawo kwananta a gidan.Domin tuni shedan ya ribace shi, duk da yana zargin ta yanka kanta ne dama don kada ta tafi, tun daga ranar ta zama gidan tamkar matarsa, wanan ne yasa ko da ya koma gida sadiya taga canji.

Wata hudu kenan da soma shiga matsalar mu da ya Aliyu, amma tamkar na shekara biyu, duk na rame na lalace har bana so inyi baki don kada suce lafiya?Cikin wata hudu ya zo so hudu duk karshen wata ke nan kwana dai dai yake yi ya tafi sam baya kulani in yazo magana fiska a

daure yake min.Ya manta da wani hakki nawa da yake kanshi, domin nima mutun ce ba ice ba, ina shan wahala da kewarsa.Darare da yawa ina zubar da hawaye don kunci da kewa, gashi yayi mun sabo da yanayin sa na rashin hakuri.Usman da Anty Abida sune kawai suka san halin da nake ciki, ko iya da amininiyata Aisha sunyi juyin duniya amma ban shaidar musu da ko mai ba.Usman ya ce, duk lokacin da nake bukatar wani abu bai min ba in tambaye shi, ni gaskiya ina da jin nauyi.Yau in na ce gashi gobe in ce gashi ba zai yuwu ba, abin da kawai na tsana shi ne inga arana babu makaranta, amma don abin anfani kamar su abinci ina maneji.Tunanin kama sana'a ya shigeni, na ce lallai ina bukatar in kama sana'a don in samu in kare DARAJAR YAYA NA, wadanda a yanzu sunfahimci tsakanina da baban su a kwai matsala.Ba kausar ba hatta Al'amin ya san cewa mahaifinsu ya canza, don watarana da ya shigo daki ya same ni ina kuka, sam banji shigowarsa ba sai naji an dafa ni.Nayi ta maza na share hawaye na na kalle shi da murmushi, ranshi a dagule ya ce, momy waye ya saki kuka?Na ce ldona ke ciwo.Ya ce, mama Abban mu ne ko?Na ce, a a Abbanku bayanan? Yace, shi ne mana, ya ce ki barshi in na girma zan maki duk abin da kike so, in kaiki maka, in sai maki komai.Na rungume shi tare da cewa, to yarona naji dadi na gode kaji.Ya ce momy ki daina kuka kin ji?

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Bayan fitar Al'amin ne na shiga sabon tunani, lallai matsala tsakanin miji da mata tana kawo rabuwar kan yaya, tana tauye yara.Domin zuwa da nayi open day din su a makaranta nan malamarsu take yi mun korafin cewa yarinyata

Kausar sam yanzu bata da hazaka kamar da.Bata da kuzari sam, ta ce kowa ya san Kausar Aliyu Tutur a makarantar nan ya san ta da kokari ga surutu, ga wayo.Haka nan duk wanda ya yi mata bata kyalewa, amma daga wancen term zuwa wanan tazama tamkar doluwa ba karatu.Bata iya rama fada, karamin yaro sai ya doke ta ta tsaya kuka, sanan tsaftar su ta ragu, a da yaran suke zuwa na daya a tsafta wanan karon sun koma na biyu.Don haka kiyi kokari ki canja kila matsalar daga wajenki ne.Afili na ce, lallai daga gurin mu ne, matsalarmu zata maida yaranmu baya, dole in kawo canji duk yanda zanyi gidan mu ya koma gidan farin ciki kamar da da taimakon Allah,Wayata na dauko na soma ruga sako kamarhaka.KALMOMI SUN YI KARANCI TSAKAKKEN YANAYI, FADIN YI HAKURI KADAI BA ZAI GAMSAR BA.AMMA DUK DA HAKA INA ME BAKA HAKURI, BA DAN NAYI LAIFI BA, SAI DAI INA DARAJA DANGATARMU FIYE DA SHEKARUNA.DA WANAN SAKO NAKE SAKE BAKA HAKURI TARE DA AIKO MAKA DA ZUCIYATA KA AMINCE DASHI DON SAKE DAWO MIN DA FARINCIKI NA.INA FATAN ZA MU KOMA FIYE DA DA, ZUMA TA ALY NAYI KEWARKA, INA TSNANIN SONKA.

Na tura mashi ina tsammanin ganin sako kokira amma shiru, duk wani tunani ko dabara nayi amma babu nasara.Wata laraba da yamma su kausar an koro su kudin islamiya, gashi dama abincinmu ya kare, nafita hannuna da Nera Dari na siyo garin rogo da suga.Nufina su sha da dare, duk da ina tunanin yaya zan sha kansu su sha gari da dare, sai lokacin da nake dawo wa yana ba yana a mota direbanshi yana janye da shi.

na shigo gidan zan Rufe sai naga mutum kamar daga sama ya nufo gida, gaba na yayi muguwar faduwa.Sam yanzu bana son ganin shi, don tsananin tsoron sa nike ji, ko sallama baiyi ba ya fara da ce mun, daga ina kike?Cikin in ina na ce sha....shago baje can gurin hadi.Yin me?Na ce,

gari na suwo da suga.Gari?Ya tam baya tare da zaro ida nu.Na sa dan yatsa na akan le buna na tare da fadin yi hakuri yara suna ciki.Sai me? Ya katse ni, na ce sai me in yara suna ciki, wato sabon salon zubar da mutunci wanan kika samo ko?Kamar ni a ce matata tana zuwa shago siyan gari?Na nufi ciki raina a dagule, in ya bamu abinda zamuci ishashshe ai ba zan fita siyan gari ba, na raya hakan cikin raina.Kai tsaye daki na shige na ajiye garin na fada ban daki don gudun kada yara suji, da gudu suka rungumeshi suna mashi oyoyo, al'amin da shi da mama, Kausar tsayawa tayi tana kallon su.Ya dube ta ke Kausar ba zakiyi min oyoyo ba? Ta ce sannu da zuwa Abba.Ta juya ta nufi dakin su.Da kallo ya bita cikin mamaki, me hakan yake nufi?Ta soma yiwa yaran sa fanfo ne?Ya mike ya nufi dakin ni kuma jin shiru sai na fito ina shigowa falo najiyo muryar sa.Kausar ina tambayarki kin yi mun shiru na ce me nene kike fushi?Sai na jiyo muryarta tana cewa, Abba ni bana so ka dawo, sabo da in kana nan kullum cikin fada da momy, ni bana son tana kuka.Itama ta soma kuka, na zaro ido cikin mamaki yarinyar,na saurara inji me zai ce, fatana Allah yasa zancen Kausar yazama sanadin fahimtar shi.Muryarshi ne ta katse ni, ok wato uwarku tana kitsa muku magana a kaina ko? Mamanku ta shirya muku in nazo ina cutarku ko?Ya sake tambayarta cikin daga murya, ban san lokacin da na fada dakin ba ina fadin haba yaya.Yanzu me ya kawo wanan tunanin?Tayaya za kayi mun wanan zaton?Na kalli kausar fita.Ta fita na maida kofar na rufe yana tsaye rai bace yana kallo na.Nayi kasa da murya tare da tausasa ta, yaya wanan sauyin da kakawo mana cikin gidan nan wlh ba sai na kintsawa Kausar ko mai ba.Tana ji tana gani, duk kokarin da nayi dan cewa basu fahimta ba amma hakan bai samu ba.Saboda ka kasa gyarawa, har takai ko a makaranta yaran sun koma baya.Hawaye suka soma zubo min masu zafi, na taka na isa inda yake tsaye nafada jikinshi na kan kame shi.Yaya ka taimaka kayi

hakuri ka zubar da makamanka ka dawo mana da farincikin mu.Ya ban bareni tare da hankade ni har sai da na fadi, ya soma magana cikin ihu.Tayaya kike so in yarda dake cewa bake bace kike bata ni a wrin yarana ba?Yar wanan yarinyar da bata gama sanin kanta ba shine har zata san matsalar wani? To ni dake dasu munsa hannu tunda kin zabi haka.Shiyasa sam bana son zuwa garin nan, saboda takaicinki, kin zama saikace sanda don Rama.
Kullun mahaifiyata tana tuhumata cewa bana kula da ku, yanzu dan zubar da mutunci wai kinje shago siyan gari.Na fashe da kuka yaya yaushe rabon ka ajiye mana abinci?Tun zuwan da ka tawo da wanan matsalar.Ya daga hannu rufe min baki, yanzu ina yi maki magana ne a kan shiga tsakanina da yarana.In zandau komai ba zan dau wanan ba, ya kamata ki sani.Ya juya ya fita bayan ya bude kofa.Kuka sosai nayi na tsawon minti daya, sanan zumbur na mike na fita.Mama tana kwance a tsakar falo tana ta tsotsan yatsanta, ita bata san me ke faruwaba.Ahmad yana zaune kan kujera ya takure, Kausar na shiga raba ido in gani, can na hangota gefen kujera ta makure tare da toshe kunnuwanta, tana nufin bata son jin abinda ake yi, ga kuka tana yi.Tayi sharkaf da majina, dakinsa ya shige shikam naje na rumgumo Kausar nazo na hadasu da Al'amin ina lallashinsu.Duk da cewa nima hawaye ke kwaranya a idanuwa na, Al'amin yazo yayi mun rada a kunne, ki hada shi da Iya kinji Momy ta rama maki(don duk zatonsu ni iya ta haifa ba baban su ba) Najasu muka koma dakinsu, na ce, Kausar Al'amin kuyi hakuri ni da Babanku za mu koma kamar da, ba da jimawa ba kunji ko? Kausar ta dago kai, yaushe momy?Na runtsi ido hawaye na kwaranya na ce, bada jimawa ba Kausar kinji?Duk suka makaleni, Al'amin yasake cewa kin hada shi da Iya ne, da sauri na ce a a ko ku kada ku fada mata, ba na ce muku bata da lafiya ba?Kuna so in taji da muwa ciwonta ya tashi?Duk sukayi shiru, nace kuna so ta mutu?

Da sauri suka ce, a'a,na ce to in kun fada mata zata mutu.Kausar ta ce, bazamu fada ba.Na share hawayena sanan na kallesu.Muna ciki har aka kira magariba, na taso su mukayi salla.Tinda na fito banga Mama ba, nasan tana gurinshi, suna ciki ko sunfita oho.Na jika musu gari suka zauna, Allah ya taimakeni suka kama sha.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Kausar tana cewa,Momy in nazama babba zan dinga siyo mana kayan abinci.Al'amin ya ce, momy ba na rigata ba.Yaya kausar nine zandinga siyan ma Momy ko mai, na ce to tun yanzu nagode, Allah ya raya ku, ku girma cikin aminci da Albarka, suka ce amin.Raina yayi sanyi yar firar nan da muka yi da ya rana sai gashi sunyi sallama shi da mama tsam ya tsaya, ganin suna cin gari.Na lumshe ido na hadiye takaici na, sannan na ce sannu da zuwa.Bai amsa ba yayi ciki, kamar in zauna sai kuma na bishi.Ya aje mama ya zauna bakin gado tare da dafe kai, na ce, ina maka sannu.Ya dubeni idanu jajur.Yaya na ke cin gari da dare?Na ce, to yaya bamu da komai ne.Na dubi mama, zomuje ki ci gari.Ya daka min tsawa, ki daina kira min sunan garin nan, ba zataciba.Ko Inyamuri ya sha gari da daddare? Wanan shine na karshe in ba haka ba rai zai baci, ban ce kala ba na juya, cirko cirko nagasu Kausar a falo.Kausar ta toshe kunne, Al'amin na tsaye cikin damuwa,nakamasu muka koma na ce su ci garin amma sai suka ce sun koshi.Kausar ta kwanto kan cinyata, Al'amin ya kwanta kan kujera na kwantar da kaina nima a hannun kujera.Wai ta wace hanya zanbi gidana ya dawo kamar da?Wa zai ban shawara dan ni ina ganin tawa basirar ta kare kan haka.Allah ka bani mafita.Muna nan har aka kira isha'i, na tashi

naje nayi sallah suma sukayi sai ga mama ta shigo da nama da Holandia, na ce, suci.Al'amin dai ya ci amma Kausar kin ci tayi waita ta koshi, na rungumo ta, Kausar kina fishida Abbanki ne? Tayi shiru, na ce ki fada min.Ta ce, eh momy shima yanzu ya daina sonmu nace, a a yana sonmu fushi yake yi in ya huce zai dawo kamar da.Sai kurum naji ta ce, wane ne yayi masa laifimomy?Na ce, ni ce, ta ce, bakiyi mashi ko mai ba, ba ma kullun kina bashi hakuri ba tunda yaki yayi hakuri ya daina sonmu.Bani da bakin magana sai shiru ina mamakin Kausar, yar wanan yarinyar har tana fahimtar abubuwa kai abin da mamaki sosai.Haka na lallaba su har sukayi bacci na kulle mana kofa sanan nima na kwanta na fada kogin tunani.
Wa she gari da wuri na tashi nayi salla da wanka, sanan nayi musu shirin makaranta, duk a dakinsu.Nace suje su gaida baban su.Kausar ta noke tare da daure fuska za ta soma kuka, na ce, haba Kausar, kuje ku gaida Babanku mana.Kina so ne ya j haushi irin jiya?Jiya ma kin ki sakar mashi fuska ne shi yasayayi fada.Ta ce, to momy yanzu tsoronshi nake ji.Na ce, daina jin tsoro kinji Kausar, yana sonku.Daga nan ki bashi hakuri.Ta ce, to.Amma sam fuskarta ba wani annuri, ina biyeda su har kofar, Al'amin ya kwankwasa daga ciki yaya ya ce, wanene?Mama da jin muryarshi sai ta ce, Abba.Ya ce mama.Na bude kofar suka shiga, yana kwance kan gado da waya a hannunsa, da Alamu cht ya ke yi.Kausar ta dan tsaya nesa dasu kanta a kasa.Al'amin ya zauna bakin gado,Mama ta hayekan gado, ya rungume mama da Al'amin sanan ya tashi zaune.Al'amin ya gaida shi, Mama ma cikin hausarta mara dadi ta gaida shi.Ya kalli kausar daga inda take.Zo nan.Ta tafi, ya janyota zuwa jikinshi, ta ce ina kwana?Ya ce, ba zan amsa ba Kausar har sai kin fada mun me mamanku ta ce maku nayi, kuke jin haushi na?Kausar ta ce ba ko mai Abba, Al'amin ya ce ta ce ne fa muzo mu gaida kai.Ya kalli Kausar, yanzu kunfi son mamanku fiye dani ko?Al'amin

ya ce, muma ka daina son mu Abba.Ya ce, ok, haka mamanku ta fada muku?Kausar tayi saurin cewa momy bata fada mana haka ba, ta ce ne kawai muje mu gaida ka.Ya dungurewa Kausar kai yar karama da ke kin iya munafunci, ba zan kara yi maki tsaraba ba.Ya kalli Al'amin, in ba ka daukar maganar mamanku zan sai maka keke kana so?Al'amin ya kama murna ina so Abba.Ya kalli mama, mama na ke kuma in se maki motar ki ta wasa ko?Na juya kicin ina kuka, mutumin nan zai raba mun kan yara, zai kafa min jam'iya yan partyn shi da nawa.Jin takun Kausar yasani share hawaye, cikin sheshekar kuka ta ce, momy kinji Abba zai sayawa su Al'amin da mama tsaraba ban dani.Na tsugunna na rungumota jikina ina shafa mata kai, yi hakuri Abbanku wasa yake yi miki zai siyo miki kinji?Ta ce, Allah momy da gaske yake yi ba ya cein fitar masa daga daki ba?Na ce, yi shiru zai sai maki.Da kyar tayi shiru.Na bata jug na ce, kije wajen Iya ki ce mata in ta dama koko ta baku, karfa ki ce mata wani abu ya faru kinji?Ta ce to.Ta tafi nikuma na zauna a kicin cikin ta gumi.Kausar ta sami Iya kwance ta gaida ta, ta ce kausar menene?Ta ce, wai in kin dama koko ki bamu, iya ta ce shine aka turoki ba Abbanku ya dawo jiyaba?Me yasa bai rakoki ba?Tayi shiru Iya ta ce to muje in se maki koko gidan ladi me koko dan kulluna jiya ya kare, kice mata na ce a jika maku gero tunda jifa jifa kuna shan kokon, ban cika son abin siya ba.Sam iya bata fahimci bamu da komai a gidan bane, tunda lokaci zuwa lokaci sukanje su amshi kokon.Ta samu masu kosai sanan ta rakata har kusa da gida.Tanaji tana fadan turota ita kadai a wanan safiyar, ta ce da uwarku tana tattalinku amma yanzu duk ta canza,na rasa me ke damunta.Suna shan koko da kosai kausar tana fada min sakon Iya, na jika gero na ce to za a jika,suka gama na dauki Mama na nufi kaisu makaranta, kusan wata guda a kafa nake kaisu makaranta, don mota tuni nayi fakin dinta gefe na rufe ta don ba mai ba na da kuma kudin siya.Ina dawowa

na tarar da shi da Usman zaune yana karantowa Usman laifuka na.Na gaida Usman na shige daki, na hau gado na kwantawa,bawai don bacci ba ko don hutu, sai don tsabar ta kaici.Can na jiyo muryarshi yana kira na, ya kalle ni.Kin san na fada maki ba zan dauka ba ki rabani da yara na ba.Jiya na shigo gidan nan wai Kausar tana yin fushi dani yar karamar yarinyar nan.Al'amin yana fada mun na daina son su, tayaya zan yarda wanan tunaninsu ne?Usman ya daga mishi hannu saurara aboki na, ka barni in gama magana ta don kada kakatse ni.Usman ya kalleni,Sadiya me yake faruwa ne?Na runtse ido don ta kaici, yaya Usman duk abin da ya faru Abban kausar shine sila.Na koro mishi komai tun daga farkon rigimar har zuwa yau.Sanan na ce yaya Usman tsakani da Allah kullun yaran nan suna kallon muna fada, ko ince daga yazo sai shiga tashin hankali zasutashi da tarbiya me kyau?Ya ce, a a.Na fada musu yanda mukayi da malamansu. Ga rashin abinci wane laifi na masa, ni dai yanxu tunda gani gashi kurun ya fada min laifi na, wlh zan bashi hakuri mu koma kamar da yaran mu suma su sami natsuwa.Usman ya kalli Aliyu, aboki kaji, sai ka fada mata laifinta don matsalar tazo karshe.Aliyu yayi mun wani kallo ke dai kawai baki son zaman lafiya ne, duk ki dauki damuwa da bakin ciki kisawa kanki.Sau nawa zan fada maki baki yi mun komai ba?Usman ya ce, to na rokeka aboki ko mai ya wuce.Ya runtse ido tare da fadin shi ke nan.Na dube shi nima in sha Allahu ko mai ya wuce.Usman ya ce, Alhamdulilla, yanzu sai ka tashi mushiga kasuwa don nima abincin gida na ya kare.Nan dai suka fita.A cikin mota Usman ya kalli Aliyu.Aboki ka canza fa,Aliyu ya kalleshi wacce irin canzawa nayi?Usman yayi murmushi sanan ya maida hankalinshi titi.Kayi kiba sanan dabi'un ka sun canza.Aliyu ya kure Usman da ido, zaiyi magana kenan wayarsa ta soma ruri, ya ciro ya kurawa Screen din ido,sha wara yake ya dauka ko ya yanke,Usman ya kalle shi, daga mana abokina,

Aliyu ya katse kiran sanan ya kalli Usman,daga jin kira sai kace in daga ba tare da kasan me kiran ba?Usman ya ce, jami'in tsaro zai ji shakkar daga kiran koma wanene.......Kiran yasake shigowa, sai kurun Aliyu ya dagadan kada Usman ya dago abinda ke faruwa.Ya ce, yaya?Mujidat ta ce, muryarka nake sonji, nayi kewarka da yawa, don Allah ka dawo yau.Tana magana kamar zata yi kuka, salon dake narkar masa da zuciya,take ya manta da wa yake tare har ya furta cewa.Kada ki damu gobe kamar yanzu muna tare,ta ce, to Zaki na sai mun hadu a internet.Sai da ya salameta sanan ya tuna yayi baram barama.Ya dubi Usman wanda bai ce kala ba, ya soma nade tabarmar kunya.Wata abokiyar aikina ce, muna gabatar da wani aikine.Usman yayi murmushi sanan ya ce, sau da dama in mutun ya shiga aikata rashin gaskiya sai kaga ya zama makaryaci.Ita ko karya illar ta da kayi so daya kafin ka fitar da kanka sai kayi kusan sau goma.Aliyu ya kalle shi, me ya kawo wanan zancen?Usman yayi dariya, ka tsargu ne?Aliyu ya kalli gefe, intsargu da me kuma?Usman ya hade rai, tsayar da halayenka haka nan Aliyu.Ya gangara gefe titi yayi fakin dazu nake ce maka dabi'unka sun canza ko? Aliyu ya kalli titi muje zuwa da maganarka, in wani zai fada mun aboki ba zan yarda ba, amma gani ina zar ginka cewa kana hulda da matan?Aliyu ya kalleshi da sauri, haba aboki, nasancewa zaka iya bada shaida cewa ban kasance mai shiga lamarin da mata suke ciki ba, bare har inyi hulda dasu.Usman ya ce to amsa min wadan nan tambayoyin.Aliyu ya cire hankici, ya share zufar fuskarsa sanan ya ce, ina jinka.Usman ya ce, na kira layinka sau uku wata macece take dagawa.Na farko da dare ne gurin karfe dayan dare, don in fada maka rasuwar kanwata, sai kawai wata mace ta daga wai ka shiga wanka.Na biyu da safe wata jumma'a don mu gaisa ta ce ka fita gurin masu gadi, na uku gargadi tayi mun in san lokacin da zan dingakiranka yanzu kana cikin halin da bazaka

iya daga waya ba.Sai na soma lissafi giya kake sha da har ba zaka iya daga waya ba, koko menene?Sanan ita wanan matar yakuke da ita har zata kasance a inda kake ciki tsakar daren nan .In zuciyata ta zargeka sai wata ta shaideka da cewa ba aikin ka bane, abin da bakayi ba kana yaro ba na zaton cewa zakayi shi da girmanka.Amma yau da matarka take fadin yanda ka kaurace mata, sai na amince kana neman mata, don kai ba me hakurin zama baka tare da mata bane.Aliyu ya hade rai tare da duban Usman, me cece shaidar ka ta zahiri?Duk abin da kafada bai zama shaidar da zaka amince ina bin mata ba.Ba zan iya zama ba mace ba, shekaru nawana dauka can baya babu auren?Usman ya ce kila lokacin baka san amfanin matan ba,amma ni shawara daya zan baka, inma zakayi harkar bariki to bai kamata ka wulakanta matarka ta sunna ba.Aliyu ya ce, dan Allah mu rufe wanan firar.Usman ya ce kafin mu rufe sai nayi maka nasiha duk da cewa bani da tabbas akan zargin da nake yi maka.Na san mutun yana canzawa kamar yanda wahainiya take canzawa zuwa duk kalan dataso.Nasihata gareka in ka canza daga fari zuwa baki don Allah ka saki wanan layin ka koma dai dai ko don gudun zunubi, ko don tsoron azabar Allah.Ko don kare mutuncin yayan mu, ko don kare lafiyar ka daga cututukan zamani.Sanan maganar zubewar daraja da kimarka a idon wayanda suka san kanayi. Aliyu ya runtse ido cikin in ina yace, muje aboki don Allah.Suna tafe yana share zufa, lallai zancen Usman ya shige shi.
Ko mai na abinci zuwa kayan tea sun hada muna, lokacin da suka dawo ina kwance kangado ina karanta littafin gidan zahra.Sau da yawa in ina karanta littatafan Hausa sukan debe min kewa halin da nake ciki, har na sha cin karo da irin matsala ta.Sun ajiye min kayan abinci suka sake ficewa, na fada kichin na shiga girki, yarama da suka dawo makaranta sai murna suke sun sami lafiyayen abinci.Yaushe rabon

muyi girki da kifi ko nama, yau gashi har farfesun kan rago mukayi.Da daddare na fada ban daki na sake wankana sheka kwalliya duk tunanina yau za a shalabari.Sai dai muka kwanciya ya juyya min baya, na gaji hakurina ya kare don haka na ajiye kunyata na fada masa cewa, yau ni ina son a faranta min.Ya ce, shi gaskiya baya jin zai iya wani abu yanzu don duk a gajiye yake.Nace, haba yaya, nima fa mutunce kamar kowa, sama da wata hudu ka juya min baya.Baka tsoron sharrin shaidan?Ya tashi zaune a fusace, kina nufin zaki bi maza? Iye? Fadamin zaki bi maza? Nasauka daga kan gadon, ban ce zanyi zinaba yay, amma zuciya bata da kashi, in na kasa jurewa fa?Na durkusa kan gwiwowina, yaya ka taimake ni ka fiddani wanan yanayin, ka tuna ni ban taba gudunka ba.Ya mike ya dauki filo.Sai da ya kai bakin kofa sanan ya ce, ina ganin kina cikin fitunananun mata bari naje falo in kwana. Rufda ciki na kwanta a kan gado ina kuka, wani mai kunci daga bisani na dangana na fada ban daki na sakarwa kaina ruwan sanyi yayi ta zuba tundaga tsakiyar kaina.Ban fito ba sai da naji sanyi yana ratsani, na fita naje kan gado na dukunkune sai zazzabi da ciwon kai.Haka na kwana har safe da kyar nayi Sallah na sha magani, sanan na fita kicin.Shi kam a ranar ya koma kusan karfe biyu ina kwance ya tsaya kaina wai ni fa zan tafi.Ba tare da na dago ba, na ce Allah ya tsare, ya ajiye kudi a gefe na tare da fadin, motarki an gyara na ce uhm.

Duk da cewa Aliyu yana kirana a waya mu gaisa yanzu duk abinda muke bukata yana kamantawa, sai dai ya barni cikin kewa.Haka nan ko a waya da mun gaisa shi ke nan sai ya ce in bashi yaranshi suyi magana,ba wata hirar soyaya ko ta rayuwa bare in sa rai zamu koma kamar da.Duk da cewa yanzu yaran nan sun dan saki jikinsu sai dai duk da haka da sun ganni cikin takura ko damuwa yanzu zakaga sunyi mun narai narai tamkar zasuyi kuka.Ni dai a bisa halin da nake ciki gara ace bukatun ya

dai na yi mun ya bani kulawa da soyayya sunfi mun duk wani abin duniya da zai sai min.Na hakura ne saboda DARAJAR YAYA NA, sam bana so in zube su inyi gaba.In ban rike suba naje can inyi wahalar yayan wasu.

Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Wata rana naje kitso inda nake zuwa a can layin zage-zagi wani gida, gidan haya ne maidauke da matan aure da dama.A kulun naje gidan ina karantar abubuwa na rayuwa da dama a gurin matan gidan.Farko matar dake yi mun kitso, sau da yawa mijinta in yadawo bata iya sakin kitson taje gurinsa.Haka zai gaji da zama ya fito ya dauki bokiti ya ja ruwa yaje yayi wanka.In kuma da abinci ya ci ya fito in ya ciro kudin cefane ya bata sai ta amsa a raine, yauma da nazo kitson hakan ne ta kasance.Ya bata dari biyu ta juyata sanan ta maida masa tana fadin gaskiya malam bazata isa ba.Ya ce ba da garin tuwo ba, kuma naga manja?Ta ce yau kwana uku muna tuwo, ta kalli yaranta dake gefe suna wasa.Habu kunji babanku wai yau ma tuwo sai suka rugo da kansu gaskiya baba yau bazamuci tuwo ba.Ya ce to me ni dai kudin nan ke nan.Ta ce, ko tuwon ne ma kudin nan ba isar muzaiyiba, ya ce haba Tasallah, ba kifi ba nama kice dari biyu baza tayi miya ba?Ya shura takalminsa yayi gaba.Ta daga murya sai dai ayi maka ciko kuma kana zuwa zaka bani kudi na.Yaran suka hau mita, shi baban nan kullun tuwo.Na kalleta cikin mamaki sanan na ce, na kusan daina zuwa kitso gurinki, ta ce zaku tashi ne?Na ce a a na ce nagaji da yanda kike daukar mijinki ba a bakin ko mai ba.Dubi yanda kike sa yaranki suna yi ma mahaifinsu rashin da'a da raini, wanan tarbiya ke nan?Tayi yar dariya hajiya kenan, Allah hajiya ba haka bane, ace mutun kullun ba ci gaba, ba

ya neman wata sana'a a caba yake.Na ce, na lura baki da godiyar Allah ta salla. Ranan fa ina kallonki da yaranki kuka ce masa kun gaji da shinkafa, san nan baki sanin mijinki ya dawo ki bishi daki ba.....
Allah sarki Rayuwar Aure,kowadai da tasa matsalar,damadai haka Rayuwar take,tanada manyan matsaloli guda hudu wadanda duka daya takan haddasa rashin jin dadi daga bangare daya,Immadai -:
Mijin baya jin dadin zama da matar,misalin Tasalla me kitso da Mijinta,kokuma...
2:Matar ake zalunta ,Misalin Aliyu da Sadiya,Kokuma ...
3:Suna zaune lafiya a junansu, Amma dangin matar ba kaunar mijin,shima Wannan Babbar matsalace a auratayya,Wacce ke Haifar da Babar Matsal..kokuma...
4 angin mijine basu son Matar, wanda nasan da yawanku kunfi sanin wanna matsalar,..
Lallai dukanin gidan auren da suka samu kubuta daga dukkanin matsalolinnan nazama wajibi Su godewa Allah,akarshe Dukkani gidan Auren dake da matsalar makamanciyar wadannan Ya Allah ka kawo musu agaji,mukuma Ya Allah kahadamu da abokan zama nagari
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347

Zaharaddeen shomar
Whatsapp 08168575100

Darajar Yayana2-04
Posted by ANaM Dorayi on 06:34 PM, 29-Mar-16
Under: DARAJAR 'YA'YANA
____________________NA

___________HALIMA K/MASHI

Assalamu'alaikum, fatan kuna cikin koshin lafiya...

Sagir Ali, Shamsusdden Usman,Fatima Ahsan,Maman Ummi,Shamsiyya,Ummi Amal,Aisha and Aisha Kaka Zanna nagode da kulawarku,sannna inna jin dadin yanda kuke kulawa da shige da ficena,shirun da kukaji yafarune sakamakon ayyuka da sukaimin yawa,fatan zakucikaba da bibiya dakuma hakuri dani. nagode zamu Dora yanzu.....

Ruwan wanka sai dai ya diba yaje yayi, wanan rashin dabi'ar har ina?tasake yin dariya, to ni in nashiga dakin in ya dawo me zan masa?Na ce, auran kiyayya aka maki?Ta ce, a a ni na kaishi gidan mu, ta ci gaba kin sani ni gaskiya ko ya dawo bana shiga, shi yanzunnan zaice zai rungume ni, niko na tsani haka,ka debo rana ka wani ce zaka rungume ni, salon su Habu su fado dakin?na ce menene dan yaranku sun ganku rungume da juna?Kai ke dai baki da dabi'a,irinku ne ake kwacewa miji cikin sauki,daga baya kizo kina ya ci amanar ki,ni dai in baki canza haliba zan daina zuwa,ta ce;to Hajiya za'a sake, ai ku hajiya cikin daula kuke baku da matsala.Nayi murmushi Tasalla kenan.Shiyasa na ce, kina da hange, ki kalli kasanki mana,Misali waccan Maman Rashidan kuke ce mata ko wa?Tunda nake zuwa gidan nan bai fi so nawa naga ta daura tukunya ba.Kullun in kazo zakaga yaranta suna cin dumame, ko garin rogo amma ban taba ganin mijinta ya dawo ta barshi ya dibi ruwan wanka da kanshi ba, ko ta shareshi taki shiga daki.Sanan sau biyu na taba ganin mijinta nasan yayi sa'ar mata, duk cikinku 'yan nan sasan da na taba ganin shigowar mazajenku da fitarku ita kadai ke yi wa mijinta sannu da zuwa da yi mashi addu'a in zai fita.Tasalla tayi yar dariya, hajiya kenan, ita waccen ai bata san kimarta ta ya mace ba, in banda haka yaushe zan zauna babu abincin kirki.Amma kina like da mutun kullum sai tayi wankan asuba don jaraba.Na ce, tafi ku godiyar Allah ne da biyayya.Sanan zakuga

cigabanta kuna nan, sanan yaranta sunfi naku tarbiya da tsafta.Tasalla ta bata rai,Hajiya mu bar maganar nan, amma ko su maman Auwal zaki tambaya matarnan tana shiryawa yaranta kinaya ne don in mutane sunzo su rinka gaidasu don a ce suna da halin kirki.Na ce, ba wani bayan aike ma ina kallon naku yaran amma baku aikensu don kunsan cewa bazasuba, sai dai ku kira nata.Daga nan Tasalla tayi kus, niko na ce in sha Allahu duk randa zan kuma zuwa sai nayi wa yaranta kwalima tunda naga yaranta basu fi girman su Kausar ba, a raina na raya hakan.Ina Mota na kusa isa gida da motar dama naje gidan kitson da mota ne, sai ga kiran Aisha aminiyata, cikin hanzari na daga ina fadin.Kin haihu kenan? Tayi dariya yau andace kullun na kiraki zancenki daya ne kin haihu?To ga yarki nan a gado.Na ce, Alhamdulillahi ga ni nan.Na kira layin Abban kausar kamar yanda na zata har ta tsinke bai dauka ba, na sake kira.Muryar mace naji cikin harshen turanci tace wakike nema?Sai da sitiyarin ya kusa kufce min, na samu na tsaya tunda cikin unguwa ne, na sake yin sallama cikin rawar murya.Ta ce kina bukatar taimako ne?Na katse layin zufa ta soma tsatstsafo min.Na rude matuka, na kifa kaina a kan sitiyarin ina fadin Allah yasa mafarki nake yi.Na kuma kallon wayar ina shawaran in sake kira ne ko in barshi, sai ga kiranshi ya shigo da sauri na daga amman na kasa magana, Muryarshi ne yanzu ya ce hello!! Dazun bakiyi magana ba sai wata irin muryanake ji.A sanyaye na ce dazun ba kai bane wata ce ta daga.Da sauri ya ce wata wa?A wayata?A'a sai dai in network ne yasa ki kika ji haka.Ya saki zancen da cewa, Ify dai?Na ce eh dama ina dawowa daga gidan kitso ne sai Aisha ta kirani ta haihu.Ya ce wace Aishan?Na ce, ta mamana.Ya ce, Allah ya raya, kin cika son yawo.Na ce to yaya in banje yanzun ba dole in sake fitowa don inyi gabadaya.Ya ce to shi kenan ina yaran?Na ce sunje yiwa iya wuni, ya ce ban son fa kina tafiya ke daya fa.Ko mama bakya iya yawo da ita sai ke daya tsura?Na ce, to yaya sun kwana biyu ne

basu je sunyi mata yini ba.Ya ce, to shi kenan kardai kiyi dare don na sanku in kuka sami surutu na ce to.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Bayan ya kashe wayar ya nufi gurin Mujidat da ke zaune kan kujera tana dafe da kumatu, inda Aliyu ya watsa mata mari sakamakon shigowa da yayi ya ganta ta daga masa waya.Ya kalleta in kika kara yi min gangancin daga min waya sai na mugu saba maki, don zaki koma inda kika fito.Ta mike tsaye kana jin tsoron matarka ne don kar tasan muna tare ta ce ta fasa aurenka?Cikin gatse Aliyu ya ce haka ne.Don haka kada ki kara daga min waya.Ya juya ya shiga dakinsa rai a bace.Mujidat ta mike tsaye tana kai kawo, wai mutumin nan yana nufin duk son da nake masa yafi son matarshi a kaina?In ma yana boye mata ne sai nayi sanadin da zata sani, in sha Allahu.Sai dai ta mutu ko ta bar mun shi, don na yi imani na fita son shi, zanyi komai don naga na rabasu da makircina kawai,ta hada yatsanta babba da na tsakiya taja suka yi kara, wanan wata Alama ce da take yi duk lokacin da ta ma kanta Alkawarin aikata wani abu cikin izza.Ni kam kwana nai da motata zuwa gidan Aisha, amma zuciyata cike take da wasi wasin abin da kunne na yaji wai netwok ne.Anya kuwa ba binne ni yaya yayi da rai na ba?Nayi murna da ganin Aisha cikin koshin lafiya tare da jaririnta.Na dauki yarainyar ina juyyata, mashaAllahu,Bello ya fiki karfin jini daga ita har Najib shi suka biyo.Na ce haka dai su mama suka ce, na ce, ina angon karnin?Ta ce ya fita na kwantar da yar na kalleta a Asibiti?A gida kafin ya samo mota har kai ya fito.Innarsu da mamanmu da ma suka zo sai kurum suka amshi haihuwar, na ce shi kenan Allah ya kawo shi cikin sauki.Na nufi wata kula dake gefe, na ce me suka barararaka miki?Na

bude kular, ta ce tuwo ne, miyar kuka, kinsan tsaffin nan sai suce wai maijego sai da tuwo.Muka sa dariya, na ce a ni na horu da tuwo gurin Iya, haihuwar kausar har wani baki nayi nayi muni dan uban nan.Muka sa dariya.tace, ai daga baya Anty Abida ta hada maki sabulu, na ce ai ta min kokari yanzu ba abin da bana hadawa da kaina.Ta ce zaki hada min sabulunma nace to, haka mukai ta fira har shida, sanan mukayi sallama naje gidan Iya na kwashi yayana muka tafi gida.
Na kasa bacci cikin dare sai juyyi nake kaso hamsin da daya na zuciyata, yaya Aley yayi min.Tabbas zan zama wawiya in ban amince yaya yana neman mata ba.Yaushe rabon da ya dora yatsansa kan nawa?Kullun dare ina kwana da kewa, hawaye na suna kwaranya.Na tashi zaune in ko haka ne wane mataki zan dauka.Zuciyata ta dauki zafi ina fidda wani huci, lallai in ya kasance haka zamuyi rigima ba karama ba, don ba zan dauki wulakanci a kan matar banza ba.
Washe gari da safe ina ta tunanin yanda zansake cewa yaya zan sake komawa gidan Aisha, saboda in na haihu kulun tana hanyar har ayi suna.Amma ni ko haihuwar Najib dinta banyi mata wani sintiri ba, yaya hanawa yayi.Kuma bana son fita batare da izininshi ba.Don nayi imani shi baya kallona Allah da ya halicceni yana kallona.Text na tura mashi cewa zanje gidan Aisha lokacin suna tare da Mujidat suna karyawa.Ya dauka ya karanta, sai ko ya hade rai ya soma kiran layi na na daga.Tunkafin in karasa sallama na ji ya ce, ban amince ba kullum fita, saboda ki dinga kallon maza ko? Na zaro ido na mike da sauri na nufi daki dan su Kausar suna nan gida don anyi musuhutu.Kuma bana so suna jin matsalar mu.Ya ci gaba da fadan shi, na ce wacce irin magana kake yi yaya?Don in dinga kallon mazaje fa ka ce?Kana nufin in na fita haka nake yi?Ya ce, oho miki, amma ban yafe ba in kika leko waje, nace naji ai tunda ka hana ba zan fita ba, amma cewar da kayi wai ina kallon mza nike son inji hujjar ka.Kana ga don ka shuka

fulawa ta fito kaki kayi mata ban ruwa sai ta mutu?Na ci gaba, haka ne zata mutu amma kasani ni nasan DARAJAR YAYA NA.Ko don su zan kare mutuncina kai shaidane budurwa gar ka bare ni a leda, ka san haka kuma kullun ina Adu'a Allah ya kare ni daga sharrin zamani.Ban jira amsarshi ba na kashe, sanan na fada kan gado ina kuka.Sai kurum naji hannun kausar a baya na tana fadin.Momy kiyi hakuri ki kyale shi.Da sauri na share hawaye na taso kausar bana ce in ina waya a daki ba ku daina biyo ni?Ta ce momy ki daina daga wayar Abbanmu, ko ya kiraki ni bana so yana saki kuka.Na ce naji muje
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Kwana uku da yin sunan yar gidan Aisha ya ta ci sunan Fateema, sai ga yaya da rana tsaka ina mamakin yanda yanzu yake son yimin dirar mikiya.Ko yana zargin ina fita ne?Oho.Nayi masa sannu da zuwa ya amsa na ce, baka fada ba gashi banyi abincin rana ba.Jiya sun bar shinkafar da na dafa da dare, sai kawai nasa a firiza yau na duma ma, amma bari in maka ko macroni ce.Ya ce barshi bani da yunwa, in na fita zan siyo fura.Sai da yayi bacci sanan ya tashi yayi wanka ya fita.Duk ina dakina ina karanta littatafi ,tinda nalura bai bukatar ganina kusadashi, nima hakan yafi min sauki don in yana gari nafi jincewa nima macece in kwana cikin kewa.Washegari ya fita zuwa gidan su Iya na dauko jakarshi, don kwashe kayan wanki wanda ya dawo dasu kamar yanda na saba.Ina daga suit din shi zan rataye wata takarda ta fado, na dauka har zan maida masa cikin Aljihun rigar sai wata zuciyar ta ce bude mana ki gani, na bude.Yar wasika ce aka rubuta da harshen turanci, ga abin da yake rubuce.ZUMA NA KA TAFI DA TUNANINA, HAR KAJE KADAWO KASANI ZA KA BARNI CIKIN KEWAR LALLAUSAR FATAR JIKINKA.BA ZAN GUSHE BA HAR

SAI KA DAWO KA SAME NI CIKIN KEWAR LEBUNAN KA MASU SANTSI TARE DA (YAWUN) KA ME ZAKI.ALLAH YA DAWO MUN DA KAI LAFIYA.....Kafin na kai karshe tuni na jike da zufa, ina gamawa na ga gari yana juya min, ban an kara ba sai dai naji ni a kasa ribin jikina a gado rabi a kasa.Kusan minti biyar sanan na tashi zaune sa sake karanta takardar ina kuka wiwi har da majina tabbas yaya mata yake bi,domin takardar ta nuna haka, mata ce kawai ya dace tayiwa mijinta irin rubutun nan, wata zuciyar ta tambaye ni ko dai ya sake aure ne?Duk da uban kishi na sai nasami kaina da cewa inda ma auran yayi zanfi son haka, da bin matan banza.Na soma kaikawo cikin gidan ina tunanin matakin da zan dauka.Shawarar wa zan nema?Na shiga dakina na fada kan gado na dauki wayata na shiga kiranshi, amma sai wani tunani ya fado min.Bari kawai in kira Hajiya Baida'u, marubuciyar littafan da nake karantawa danneman shawara.Dan ita bata sanni ba balantana inyi zaton zancen zai iya yaduwa, sanan tana da basira nasan zata sani a hanya.Ringing na biyu ta daga, ta daga muka gaisadama na saba kiranta, na ce Anty ina nemanshawara ne.Leta na gani a jakar me gida na wanda ke Alamta cewa yana tarraiya da wata mace.Ta danyi shiru na dan lokaci.sanan ba yan wanan letar kina da wata shaidar?Sanan can dama halinsa ne?Na ce, a to a da can ba na zarginsa, sai da ga baya na soma zarginsa domin Anty kwata kwata ya kaura ce min kusan wata shida zuwa bakwai yanzun,kuma Anty shi mutum ne mai zurfin sha'awa, ba zai iya daukar ko kwanaki ba ba tare da mace ba bare watanni.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ta ce kuma ba gudan sa kike ba har hakan ta faru?Na ce wlh Anty Allah ya sani ban ta ba juya masa baya ba, har matsalar nan ta shigo.Ta ce,

kuma kina gyara jikinki ba ji yayi kin zama wata iri ba?Na soma lissafo mata abubuwan da nake hadawa, ta ce, lallai kina kula da kanki.Na ce, anty yanzu in yazo in fada mashi takardar don yasan na sani?Ta ce, a a tunda kinga zarginsa kike yi kenan baki da tabbas, ki boye takardar kuma ko a idonki kada yaga damuwa.Ki bishi a hankali, ki boye sirrin nan tunda uban yayanki ne.In shaAllahu sai kiga Allah ya dawo maki dashi kan hanya, na ce,Anty zanyi yadda kika ce, amma zan ci gaba da bincike.Ta ce, za ki iya amma ki sani tsananta bincike shima matsala ne, don zaki iya ganin abinda zai saki hawan jini, na ce anty in na tabbatar da gaskiyar zan tunkareshi ne in nuna masa nasani.In ma zai aureta ne gara ya aureta da zaman banzan nan, ta ce haka ne, amma kada ki manta da adu'a, na ce insha Allahu, ina magana cikin kuka.Ta kwantar mun da hankali da cewa, ki daina kuka, na ce anty me nene maganin bakin ciki?Ta ce karatun Alkur'ani zuciyarki zata wanke sarai.Na ce, to anty na gode.Muka yi sallama na kwanta nayi kuka sama da minty biyar sanan na tashi na boye takardar na ci gaba da aikina ina kuma ci gaba da kuka.Wanan wane bala'ine Abban kausar ke son jefa ni, ni da 'YA'YA NA?Ya manta cewa duk abin da kayi da Dan wani kaima sai anyi da naka?Da na koma daki sai naji komai nasa kyama yake bani, shi kansa yanzu kyamarsa nake ji, na karasa kwashe kayan nasa ina yi musu kallon su kansu suna dauke da zunubin zinar da yake yi.Tunda su Kausar suka shigo naga sun tsura min ido ita da Al'amin shine ya soma magana.Momy me yasameki a ido?Na ce, ba komai, ciwo yake min.Sai naga sun kalli juna.Na tsugunna tsakaninsu menene?Na tambaye su tare da yin dan guntun murmushi da na kirkiro ko nace yake.Al'amin ya ce, yaya kausar ce tace bata so Abba yazo in yazo yayi ta saki kuka, kuma fa ko an tambayeki sai kice ba komai shi ne nace ai yanzu ya daina.Amma muna zuwa sai muka sameki kinyi kuka, ku,ma muka tambayeki sai kice ba komai.Kausar ta ce, na canka ko Al'amin?

Abban nan ni bana sonshi yanxu.Al'amin ya bata fuska, nima bana sonshi, bakin ciki ya turnike ni, bana son kallon da yara suke yiwa mahaifinsu.Nace kausar ku daina cewa bakwa son mahaifinku,bana fada muku in kunyi Sallah ku rinka adu'a Allah ya kawo sauki cikin lamarinba? Allah yana amsar adu'ar kananan yara, sukace munayi sosai Momy kullum.
Ko da ya shigo kasa kallonsa nayi, ganinake zan iya cin kwalarsa, don haka na sa kaina a daki na rufe tare da sa sabon kuka.Ya kalli su Kausar, ina mamanku?Al'amin ne ya ce, tana dakinta, yazo ya buga kofar kamar kada in bude amma sai nafasa na bude
Ya tsura min ido lafiya?Na kalleshi, me ka gani? Ya ce, fuskarki na gani a kumbure, na taba baki sanan na shafa fuskata.Kila baccin da nayi dazun, ya ce wanan kumburin baiyi kama da bacci ba, ya fi kamada wanda yayi kuka.Na mai wani irin kallo.Don yanzu bani wani ganin girman shi, na ce ai ban san tsawon lokacin da kuka na zai dauka ba kafin ya tsaya.Ya ce to Allah ya kyauta, ya juya tare da fadin to a zo a bani abinci.Sai da na dan bata lokaci sanan naje na shirya komai na dawo abina.Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa
Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Washe gari ya fita, sai dai duk Aliyu a dame ya bar garin ya rasa gane kukan da Sadiya take zabgawa, nashi ganin bai san yayi mata wani abu ba tun zuwan shi.Rashin kulata ai ba yanzune farko ba, to kukan na menene?Dole Akwai wani abu, abin da yasake birkita masa lissafi yanda ko wayarta yakira sam bata iya dagawa.Rana ta hudu da komawarshi, ya gaji ya kira kayin Usman ya fada masa halin da ya bar Sadiya, da kuma rashin daga wayarsa da take yi.Yamma likis inayiwa kausar kalaba na wanke mata kai ina cewa sai gobe zan kaita kitso, sai ga Usman.Muka

gaisa sannan na ce, shigo falo, kausar kuma nace suyi wasa a nan tsakar gida.Usman ya kalleni, mijinki ya ce baki daukar wayarshi, kuma ya tafi ya barki cikin kuka.namike naje na dauko mashi takardar da na gani cikin kayansa.Shi kanshi Usman kasa dago kai yayi ya dube ni, can ya ce, lallai abin da nake zargi ya tabbata, amma don Allah ki kara hakuri kuma in sha Allahu ko mai zai wuce. Yanzu bari inje da takardar nan saboda bincike, na ce yaya kayi hakuri kabar takardar nan a hannuna saboda ta zama shaida a duk lokacin da na masa zancen ya musa.Usman ya ce nima da ma don hakan naso na aje ta guri na, amma ajeta gunki, na amsa sannan mukayi sallama.Ya kira Usman dan jin yaya?Usman ya ce ta ce mun ba komai tana bukatar hutu ne da dago waya, Aliyu yayi shiru, mamaki yake ji, kuma yana ganin kamar da wani abu sun hada bakine ita da usman.Aliyu ya ce, amma bakayi mata fada ba, in ita ta manta cewa mijinta nake ya kamata kai ka tuna mata. Usman ya ce, aboki yanzu kaga aikinike, kasake kirana wani lokacin.Ya katse wayar ba tare da ya jira amsar Aliyu ba.Afili ya furta cewa, tabbas akwai wani abu.
Tabayanshi Mujidat ta rungume shi.Dear wai me ke faruwa ne?Tunda ka dawo na kasa gane kanka.Ya kalleta cikin zargi kin sake daga wayar matata ko?Tayi rau rau, wlh Honey ban daga ba, ta somayi masa wadan su wassan ni tana rada mishi a kunci me yasa ba zai mata irin son da take yi masa ba?Ita fa zata iya mutuwa a kansa, amma shi yafi son matarsa da ita.Ya hankadeta tare da fadin dan Allah barni ta yaya ma zaki hada kanki da matata?Matar sunna wacce ke zaune don ni kadai, ta soma kuka tunda na hadu da kai na daina hulda da kowa, nima ina zaune nan ne dan kai daya.Aliyu ya ce, ban tabbatar da hakan ba, tunda dana fita zaki iya fita, ta sake dawowa ta rungume shi, na rantse bana bin kowa kai daya nake so da kauna.Kuma bazan daina sonka ba har na mutu.Aliyu ya zauna kan kujera tare da rike kai, itakuma ta kwanto a

kafadar shi.Tunani take yi a zuciyarta yanda zata ban bare ma'auratan.
Ina zaune ina danne dannen wayata, nima ina son bude shafin nan na fcbk don ganin me duniya take ciki?Aisha kawata da Anty Abida duk suna ciki har Aisha tana bani labari wai da akwai malamai sosai.In shiga nan in shiga nan dayake ina da karanbani sai gani na bude fcbk, banyi anfani da sunana ba ko adareshi na.Bayan kwana biyu sai ga Aisha ta zo mun yawon Arba'n, na nuna mata ta ce, ai na gani kin turo min sako, na ce yau she?Ta ce duk wadan da kike da numbar su za su gani, in kin bude, na zaro ido, har da Abban kausar?Ta ce sosai ma, amma ba lallai ya lura ba tunda bakiyi anfani da komai naki ba.Ta nuna min yanda zan dinga komai, bayan tafiyarta da dare ina kwance, na shiga fcbk nan na shiga frnds, dinsa, mace daya na gani Mujidat.Na shiga profile dinta hotunan da tasa nata yana daga cikin wadan da sukayi like wani gurin ma har yana cewa kin yi, sanan ga hotunan shi kala kala cikin photos din ta wasu ta rubuta one an only, wasu ta rubuta my Husband.(Tofa)
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com
Kokuma ku kasance taredamu a facebook
https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Na tashi xaune wai ya aure ta ne? take kaina ya sara, duk da ina cewa gara ace auranta yayi fiye da ya neme ta sai na samu kaina cikin wani tashin hankali mai tsanani.Na soma kiran layin Ya Usman ba tare da na damu cewa dare ya dan soma ba,cikin kuka nike cewa ya Usman ina ganin fa auranta yayi bai fada mana ba. Yace,Habadai wacece? Na karanto masa komai yace, kiyi hakuri ki kwanta zan bincika,kada ki kara hawa fcbk din,kurum ce masa nayi to amma muna yin sallama dashina tura mata frnd request, cikin sa'a ta amshe ni, da yake ita ma na ganta online.
Nace ban ga tasa marriage ba amma naga hoton mijinta, ta ce eh za dai suyi auren ne, nace ni yar

kano ce ita fa? tace Lagos, amma yanzun tana Illorin a gidan wanda zata aura.Kuka wiwi na dinga yi yanzun menene abun yi? na tambayi kaina, ta tambayeni ina da miji? sai nace mata bama tare, tace ayya, yakamata mu daidaita.Ita in sunyi aure bazata taba yarda su rabu da mijinta ba don tanaji ko uwàr da tahaifeshi bata kaita sonshi ba,ai ina gama krt na sauka daga nrt na soma rero kuka tare da yin danasanin wannan bin diddigin.Alwashi na sha duk randa yazo za'a yi mai yuwuwa. Ba zan zauna ina wulankanta ba haka kawai a debo ciwon zamani a kawo min yarana su zama abun tausayi,na sake zama cool ko yaushe cikin krt alkurani yana wanke min zuciya, don haka yanzu bana daga wayarsa sai dai in yaransa na kusa ya kira na mika ma Kausar nace ta dauka.Ranar Kausar har tambaya na take Mommy meyesa ba ka daga wayar Baban ko yana mki fada ne? Nace a'ah munyi maganar cewa yake in Kundawo zai kira ku ne,a haka muka kwashe wata, ranar kwatsam sai gashi, mamaki da naji banda Mama ko Al'amin bai je ya masa oyoyo ba?nima batare da na Kalle shi ba nace sannu da zuwa, yace Yauwa ya dubi yaran yace Al'amin baku ganin bane, nukamun ganka Abba sannu da zuwa.Yayi cik ba tare da ya amsa ba ransa ya baci sosai da wannan ko in kula din iyalanshi suka mishi,don haka ya dauri aniyar Cima Sadiya zarafi yau dinnan, nasan dole zai yi wannan tunanin dan haka na hada ma yara kaya na kwana daya nace suje gidan Iya su kwana tunda sati ne gobe, suna fita na kulle gidan na shiga fall na kulle kaina na cire key din na nufi daki,ya cire kaya sai gajeren wando zai shiga wanka,nace toh Abba kausar yau fa zamuyita ta kare a gidan nan ko ni ko kai?ya juya yana min kallon mamaki sannan yace ke ina zaton kin soma shan fakalin ko?nace 'eh wai don ma ba Zina nakeyi amma ka bani kunya, ba tsoron Allah ba kunyarshi baka tunanin darajar yayana ka aje karuwa a gidanka Kuna fasikanci,saukar Mari naji tau,sannan yace in ji wane makaryancin, na rike kuncina ka mareni Akan wata 'yar iska, toh bazan

iya zama da fasiki ba ka dinga azabtar dani a kan karuwa na warware gefen zani na ciro yar takarda na mika mishi, ga aikenta zuwa gareni, sannan na dauko wayata na same shi yana krt takarda duk jikinshi yayai sanyi, nayi maza na fito da pics dinsu da nayi saving, wannan ma karyace ba hoton ku bane?na soma kuka ka cuce ni ka cuci yarana haka kake nufin ayi ma Kausar?ya daka min tsawa kina hauka ne kike ambato sunan yata cikin wannan maganar?nace ba dadi kake ma yar wasu?Na sake fashews da sabon kuka ka bani takarda ta, bazan iyazama da kai ba!kina haukane zaki ce na sake ki,toh bazan iya ba me Zancewa Iya?nace in itace matsalar ka bazan fada mata komai ba in baka sake ni ma zanje yanzu in fada mata! hanklainshi yatashi ya dauki jallabiya ya sa nikam ficewa nayi naje dakina na sure hijab na bude Kofan falon ya rike ni kina hauka ne zaki je ma Iya da wannan zancen?nace me zai hana,ya kamoni na kwace nayi waje na bude kofar gida kafin na bude ya daukoni cak,dakina ya jefa ni kan Gado yace kina hauka ne?yace nayi laifi kiyi hkr ki nutsu Muyi magana, nace kai ni fa na daina Sonka kuma girmanka ya zube a gurina, ganin zanga-zangar tayi yawa sai ya kulle ni ta baya ya daga waya ya kira Usman yace don Allah yana son ganinshi yanzu a gida,ina jinsu a falo yana fada ma Usman shi bai San ina ji ba wai duk na daga hankalinta har wai ina kwacewa ni dole sai naje na fada ma iya.Usman yace aboki tambaya daya zan maka kayarda kana aikata laifin nan?yayi shiru ,Usman yace in har ka iya amsarwa shine zai kawo karshen matsalar, yace toh ai na fada mata cewa naji na kuma amsa laifina don haka ta tsaya Muyi magana taki,Usaman yace a'uzubillah, Aboki me yarude ka ka fada wannan harka?wlh aboki kurum na tsinci kaina a wannan halin, ka San zuciyata bata da Kashi ga kuma sharrin shaidan, Usman yayita masa nasiha sannan yace a jira ni na fito fuskata suntum nace Nifa Usman na gaji ba zan zauna ba,Usman yace yi hakuri nasan kinyi hakuri kuma inshaAllah bazai kara ba,na kalleshi nasan zai

chigaba kawai ni gara ya aureta in son aure suke,inkuma matan da yake bi da yawa toh ni bazan iya zama ba.Usman ya Kalle shi gaskiya ne Aliyu yace ita kadai ce muke tare wlh kuma itama tsautsayi ne, Usman yace ko kayi nadama sanin zaka koma can ku sake haduwa shi yasa ta kawo shawara cewa taje tayi istibrai in ya so sai Kuyi aure.Aliyu yace ina bazan auretaba ni nakuma yi miki alkawarin cewa mun rabu da ita inshaAllah, a gaban mu yayi waya ya kira maigadinsa yace a fitar da Mujidat daga gidan kafin ya dawo, itama ya kirata yace mata ya gode da wasikar da ta sa mishi a cikin kaya don ta raba shi da matarshi don haka maza ta bar mishi gidanshi,bai jira takare kanta ba ya kashe dukkan phones dinsa.
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
Ni Sam bai wani Burgeniba,suna cikin gidansuna ta bani baki har magrib,suna fitowa nayi wanka na sha magani nayi sallah ina zaune kan dadduma har sai da nayi sallar Isha dama banyi girki ba,na hau gado abuna na chigaba da kuka, na soma barci naji ana shafa ni a wuya abunda na jima ina kewa amma sai naji tamkar ana shafa min kaya.Na ture hannunsa a kunne ya rada mincewa'My choice zan zame miki sweet Aly dini har abawa ba zan sake chanzawa ba,natashi zaune muna kallon juna cikin ido nace yaya Sam yanzu in ka fadi magana bana yarda matsalar mutum ya kama karya kenan har a gane shi,na sauka daga kan Gado naje na jingina da bango ina kallosnshi shima ni yake kallo nace yaya ni fa nadarmarka bata shige ni ba don nasan dole sai Kun sake haduwa da yarinyar aurenta kawai shi ya fi dacewa da kai,ya nufoni amma ina ce an gama maganar nan,bazan iya auaran ta ba har ta Haifa min yara na gari Domin ba uwa ta gari bace,itace tayi ta bibiyata har sai da komai ya faru kinga kuwa in na aure ta ta kuma ganin wani

shima xata iya cewa tana sonshi,ya kama hannuna ki yafe min mukoma kamar da, Abban Kausar na hkr amma sai Kamin rantsuwa cewa bazaka kara aikata wannan halin ba?
Cikin sauri yace'na rantse ba zan sake ba nayi alkawarin, nace toh shi kenan na zame hanuna naje na kwanta sannan nace yawuce, ya Tako ya zo ya hau gado ya kawo nizuwa jikinshi na tashi zaune yaya kayi hakuri bazan sake iya hada shinfida da kai ba har sai kaje kayi gwajin cutar kanjamau!!!!! Zumbur ya mike tsaya tare da rike kanshi Sam baiyi tunanin wani HIV ba tunda yake tarayyada yarinyar, ya fara sintiri a tsabar dakin,nace da baka yi tunanin haka ba ko?ya sauke ajiyar zuciya 'ban yi wannan tunanin ba wlh Sadiya amma bana zaton tana da shi,tunda tsawon zamnmu ban taba ganin tayi wani ciwo ba,nace ba a nan take na, Ance mace tana yin shekara goma ciwon bai nuna ba,kawai kaje kayi gwaji in ma tanashan magani a boye wa zai sani? zufa ta rufeshi sai lumshe ido lallai kamar yana ganin ta tana shan wasu kwayoyi har ya taba tamabayar tace na family planning ne,fita yayi da sauri na tashi na biyo shi ina cewa ina zaka Abban kausa'r yace'koma asibit zanje yanzu nan........
Ku ziyarci blog dinmu domin karanta Littatafai masu nishadantarwa Anamdorayi.mywapblog.com Kokuma ku kasance taredamu a facebook https://mbasic.facebook.com/HAUSA-Novels-389304544597988/?_e_pi_=7%2CPAGE_ID10%2C737012347
toh fa sai ku biyo ni cikin Kashi na uku don Jin ya xata kaya shin Aliyu yana da ciwo?taku Halima K/ Mashi

Zaharaddeen shomar
Whatsapp 08168575100